🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Free page:01

KANO STATE.

*Unguwar kwanar ƴan dadawa*

Tafe take tana ƙwambo,ta ɗage kafaɗarta ɗaya irin yadda nigogi keyi,jikinta sanye da wata ƙatuwar riga irinta maza da wando shima ƙato,kanta sanyeda pcap,zariyar wandon harkusada gwiwar ta,ƙafarta sanyeda wani ƙaton boot na maza baƙi, duk ya tsufa yasha faci,kayan jikinta kuwa sunyi uban squeezing,se ƙwambo take tana hura hanci,tafiyarta ma tanayi rana ɗage kafa ɗaya kamar namiji,hannunta riƙeda ƙaramin bucket fari wanda ake cewa fallasa na talla,shaƙe yake da awara me miya.

Tana tafiya tana ɗage kafada irin yadda maza keyi,duk inda ta gitta yara da manya sekaji ana kANDE mai awara,ita kuma tana ɗaga hannu kamar wata ƴar siyasa tana faɗin "eh mana,dawa dai, kuhuta kawai".

Tana kawo wa wata chamber samari guri ya kaure da ihu suna faɗin zaa kand, zaa kand,itakuwa se wani ɗage kafada take tana ƙwambo,tana basu hannu suna kashewa kamar yadda maza ke gaisawa da junansu.

Cikin karkace baki kamar namiji tace "eh maza yane?, ya ake ciki ne eye?,kun haɗo min balance ɗina ko yaya?"

Ɗaya daga cikin samarin yace "ai tuni na cake miki uwar kuɗin ki zaa kand, d one nd only ƙanwar maza in the ƴan daddawa village" wani juyowa tayi ta kallesa ta karkace baki ita adole namiji ce tace "zakarius asswear zan bubburma maka hannu a hanci,see zis tsamius want to read me nonsenseus eh,tsohon waye yake a village din iye? Zakarius zafa mu raba tawun(town) da kai fa,Allah wlh, Ni kar ka sake cewa unguwar mu village garama kawai ka mata zigidir ka kirata local getto yafi yawwa", tafada tana wani dire bokitin awarar ta.

Tamika maka hannu tace "giv me zaa yastazey(yesterday)balans",miƙa mata kuɗin yayi,ta amsa ta gyara p cap dinta ta laƙwato miyau tafara ƙirga kuɗinta.

"Wan,su,siri,foo,fai,sis,sabin,ess,nai,sen" haka ta dinga fillila ƴan hamsi2 tana kirgawa ita adole turanci take,samarin wurin sunmata yuuu da ido suna kallon ɗan bakinta kamar gidan tsutsa gashi jajur wai ita anan namiji ce,kaf faɗin unguwar batada ƙawa duka maza ne abokan hurɗarta,acewarta ita ƙanwar maza ce sbd haka itama namiji ce ba ragguwa ba,ƙawarta ɗaya ce layuza,itama sbd tsananin haƙurinta da juriya yasa suke ɗasawa,saboda tun suna yara ita kaɗai ce take jure wahalar bala'in kande shiyasa har suka girma suna tare,kuma bata sauyaba duk ko yadda suke da mugun banbanci in person. Iyayen layuza sunyi2 suraba wannan abota saboda yadda kande ke tafiyar da rayuwarta kamar ba mace ba, komi nata a tsaitsaye take yinsa tamkar namiji kasancewa duk yayyenta su takwas maza ne,ita kaɗai ce mace,se yaran kawunnanta mata biyu.

Wani siririn saurayi ne yazo chamber yana wani hura hanci,tana tafiya yana kakkaɓe wandonsa da hankacif,ta inda ta ajiye bokitin awarar yabi ze wuce,be Ankara ba ta finciko rigarsa ta baya da hannu ɗaya tadawo dashi inda take tsaye tace "kai yane? Bakaga manyan guys bane zaka wani taho siii kamar dodon koɗi  kana nema ka yimin tamola da bucket of my awaras" cikin broken english dinsa yace "hey u mara foka, liv my t-shirt alone,wat do you say,i will eat ur fada, daughter of air kawai".

Cikin ƙaraji tace "hey wat do u nufi iye? Is me ka kira dota of air iye? Hey gayis ku cafa min shi anan gurin,Ni ze nunawa karyar turanci harda zakigina,kamar ni zaa soja of gidan ustazu habu me kayan koli,zecewa dota of air,nice ƴar iska,dama ɗan iska kace dana maka afuwa,gayis oya ku tara masa na yashi abaka" aikuwa rana rufe baki ɗan kanzaginta zakarius ya fizgo wnn lamushshsem saurayin yafara talle masa ƙeya,yana faɗin "hu are u iye?,do u know zaa soja of ƴan daddawa getto iye,zis is zaa kANDE, me awara and  zaa one nd only soja of zis tawun".

Dasauri wani saurayi ya taso yana cewa "easy zaa kand, baki gane wnn bane eh?".

Cikin hura hanci ita adole uban daba tace "hey Boris don't firgita me, don't do yawa,kawai ka bari nasa zakarius da duna sumasa ɓalli-ɓalli a hammata,Allah wlh yanzun nan se nasa su mayar dashi kangaroo hannuwa aɗage" tafaɗa tana keɓe baki gefe.

Boris yace "dawa de zaa kand wnn fa she is jikan mai unguwa Bello,kin mantashine?, tun muna yara aka kaishi bauci karatu gurin ƴan uwansu,baki gane shiba?".su adole se sunyi turanci,dama haka suke duk ƴan gang din kande Mayun turancine,dolema kayi turancin nan na dole inde kana tare da kande.

Se lokacin taƙare masa kallo tace kai "Bello sagalo, innalillahi wai wnn Bello sagalo ne wanda yake shan majina muna yara, innalillahi yee gurin ya kaure da ihu,Bello sagalo haka akayi ta ihu ana kashewa,suna tambayar sa yakaratu, yanata zuba musu ƙarya yace ai yagama degree dinsa a harkar noma,shi yanzu she is piropeshonal farmer ne in d ƴan daddawa tawun.

Kallonsa kawai suke suna ta ihu yana basu labarin ƙarya bayan ance musu almajiranci aka kaishi,amma se gashi yana ce musu shi yagama degree dinsa,se zabga musu turanci yake.

Kande ta daga murya tace "oya kip kwayet,oya zakarius ɗauko min awarar cen kowa yasiya kuma yau ba bashi wlh, asawata(mamanta) tace kitty zatakai hospital bcos of she is not well,sbd haka kowa yau seya biya zeci".

Boris yace "dawa de zaa kand wlh yunwa nakeji kuma banda ko ƙarfanfan yau,yau emti nake alqur'an,atemaka abani har gobe" kallonsa tayi tace "yawa kake zakarius eh,meye haka ne,Allah yau sede Kaci tuwon asawarka,kanaji fa nace kitty ba lfy yau Allah no loan of my awaras".

Nan danan aka wawashe awarar suna tsaka daci Bello jikan me gari yace "kawarmu amma awarar nan wlh da dadi" cikin jin haushi tace "kai sagalo wlh zansa zakarius yamaka askin rabin hanci,dan me dafa muku tuwo agidanku  wanene kawarku?, ni am soja,zaa one nd only soja of gidan ustazu habu me kayan koli,ko kace zaa kand,da nayi niyyar nayafe maka kuɗin awarar amma nafasa,kuma wlh dan ma awarar ta shekaran jiyace datafi hk daɗi".

Duk kallon ta sukayi jin abinda tafaɗa wai awarar ta shekaran jiyace,masu lashe hannu duk aka tsaya ana kallon.

Sauran guda huɗun da ta rage tace zakarius ya ɗauka ya cinye tabashi kyauta.

Wato ita kande haka take duk bala'i seta fadi gsky sede a mutu.

Gata da kyauta,abunta baya rufe mata ido sam.

..........

Hanyar gida ta nufa bayan tagama haɗa kan ƴan cinikinta,tana tafe tana wakar  bobmali tana wani buɗa kafaɗu,duk inda ta gitta zakaji ana zaa kand tana Sa'a de mutanena, tana ɗaga hannu kamar meneman ƙuri'a.

Dede wani gida madedeci yasha suminti taja birki ganin maza na fitowa daga zauren gidan nasu da alama yanzu aka idar da sallar azahar,dama idan aka aka zauna ɗaukar karatu agurin babanta se anyi sallar azahar sannan ake watsewa, gefe taja tana fito se wani kallo mazan da suka kasance samari da magidanta harma da tsoffi suke mata,wasu na mata kallon tir da ita batayi halin ubanta ba wanda yakasance babban malami a unguwar kuma liman.

Yayinda wasu suke mata kallon marar kamun kai kuma marar hankali,wasu ma kallon da suke mata ma'anarsa aboye take.

Ganin sungama wucewa ne tazo tana bouncing tashige cikin gidan itama,a zauren ta haɗu da babanta mlm babu me kayan koli,tana shiga tace "Sa'a de dagus, zaa imamu sannunka de da hutawa" kallonta yayi murmushi kwance akan fuskarsa cikin Muryar ustazai yace "a'a ya kande,ainafin daga gurin tallar ake ne?"  "Dawa de dagus,dagacen nake kuma an siyar,duk da na faɗa musu ta shekaran jiyace amma haka suka lamushe suka caken balans ɗina,kasan innata akwai iya sarrafa hatsi,duk taurin kan hatsi yana tsoron masifar inna,shiyasa kaƙi kara aure dagus,hehehe Kai dagus nawa,zaa imamu sekayi Allah wlh" tafaɗa tana keɓe baki gefe tare da sheqewa da dariya ganin yadda baban nata sauke tabaransa yana mata kallon ƙasan ido.

Cigaba tayi "wai dagus ina zawarar nan taka ne batula iye? Kasan fa cikar nan tana bala'in ƙaunarka iye, she is love you lodi lodi asswear,yawa kake imamu,kawai karufe ido kayi wuff da batula,kadena tsoron inna ni na tsaya maka,kalli batula ƴar caras da ita eyane" ganin tana neman gurin zama yasa cikin lallashi yace "ainafin yake uwata kisamu kishiga daga ciki ki kai kuɗin tallar naki,seki samu ki watsa ruwa ajikin ki ko yaa kande" sheqewa da dariya tayi tamiƙe ta ɗauki bokitinta tace kai innata Allah yasa de ƴar aljanna ce,duk ta rikita mana zaa imam da bala'in ta,imamu guda amma yana tsoron matarsa hehehe" takara sheqewa da dariya tana fito.

Ball take da duk abinda yatari gabanta,tana faɗin "asswear Sena saka ƴan gidan nan adashen robobi,tunda kun zama non living things,ko Ina se kun karkasa kaya sekace gidan kutare, ƴan yawa kawai, Alqur'an inde bazaku zama living things ba sede kuyita siyan sabbin kaya,dan kullum Sena fasa wanda nagani a tsakar gida", wata matace tafito daga ɗakin ta tahau durawa kande zagi ganin tayi mata fatali da sabon bahonta data jiƙan kayan wanki,gashi se yararin ruwa yake da alama ya fashe ne.

Ko kallon inda take kande batayiba ta afka ɗakin innarta ko cire takalman ƙafarta batayiba,wani baƙin cikin ne ya tokarewa umma amaƙoshi ganin ko kulata kande batayiba duk irin manyan ashariyar datake sauke mata,ga sabon bahonta agefe ruwan ciki yagama tararewa aƙasa sbd babbar hujewa  da yayi,ƙwafa tayi ta juya ɗakinta inda tabar baƙuwarta.

Aɗakin su kande kuwa, tasamu innarta ta idar da Salla takalleta tace, "uwar masu gida ya akayi naga bokiti, incede ba bashi kika rabar da awarar ba yauma?" "Ga balans ɗinki nan yau ba arnen dana baiwa bashi,kowa seda yaban ƙudina,kuma na gaya musu awarar shekaran jiyace datayi cimbi amma dashike hannunki na daurine sunsiye harda lamushe hannu,kai inna  hoo ke,hoo ke ga masifa ga iya girki,ga kyau kamar birin wasa,zaa inna ta,matar imamu,kin mallake mana liman guda duk masifarki amma yaƙi kara aure,yafita gari ana girmama shi,amma daga shigo gida seya koma kamar zakaran da ruwa yayiwa bugun dawa,kai inna Allah de yasa kishiga aljanna" tafaɗa tana shafa ƙatuwar magen dake kwance akan gadon innarta ta,duka inna ta kaiwa kande ta goce tana dariya tace "zanci ubanki fa uwar masu gida,nikike fadawa Allah yasa zan shiga aljanna? Yo idan aljannar ta ubankice kice karya sakani".

"Sa'a de inna kema kin san idan aljanna a hannun dagus take da tunkan ki sheqe ma ze wullaki cikinta,Kodan jarabar ki,ni jiyama batula ta tareni a hanya tace ina imamu nata,harda sabulu tabani" da gudu inna ta biyo kande aikuwa takwasa aguje se dakin kakarta Amo,kan ta shige ɗakin tasakeyin ball da bahon umma na ɗazu aikuwa yarabe biyu,ko waiwayawa batayiba ta afka ɗakin Amo kakarta, cikin ihu irinta bebaye Amo tace "na shiga uku takwara, waya biyoki ne kike neman kayar dani?".

Acen waje kuwa inna wani aikin takama ta fita batun kande,dan tasan ko giyar wake tasha bazata fara binta ɗakin Amo ba wacce yaran gidan suke kira da gwaggo,dan ko bazata bari ta daki kande ba koda lefin me tamata balle yanzu da suke ba'a.

Tana cikin haɗe kayan wanke wankenta Sega umma ta fito daga ɗaki ta rako baƙuwarta kallon banza sukayiwa inna suyi hanyar zaure, umma se sakewa inna habaici take.,

Ko ci kanku inna batace musu ba,sukayi hanyar waje suna ƙus-ƙus,cikin ƙasa da murya umma take cewa,"dan Allah lami ki tabbatar kinje min gurin nan,wlh kullum na kalli waccen shegiyar me suffar maza banajin na gamsu,sonake talalace takoma kamar karya,ganin ta ahaka be isheniba sonake takona magajiyar" takarasa tana kashewa lami ido,shewa sukayi suka tafa.

Koda umma tadawo daga rakiya tasamu bahonta adagargaje wata ashariya me rai ta lailayi tana sakewa,"wani ɗan kaza kazane ya dagargaza mata sabon bahonta,wane tsinanne ne,ɗebabbe,tanbaɗaɗɗe", tanayi tana karasawa kusada inna,tana zuwa ta duƙa ta dau fasasshen bahon nata tana bangaje inna ai kafin tayi motsi ba biyu inna ta kwashe ƙafarta Sega umma aƙasa kamar an juye buhun dawa,ihu tasaki dede Lokacin da ƴarta Ikilima ta sanyo kai,ganin uwarta aƙasa tana zabga ihu ga inna agefe kamar batasan abinda akeyiba dan ko kallon inda umma take tule aƙasa bata kallo kamar ba ita ta juyeta aƙasanba.

Aguje Ikilima ta rugo tana faɗin "innalillahi umma sannu,garin yaya kika faɗi,gashi dan baƙin hali bawanda yatemaka miki" tafaɗa tana zabgawa inna harara, cikin kururuwa umma tace "ga baƙar  muguwar data kwashen ƙafa nan,sbd nayi magana akan tsinanniyar ƴarta me suffar maza,ta fasamin baho,wayyihuhu kashin aguɗina ze balle,yiiiihiii duwaiwaina".

Cikin masifa Ikilima tasani ummanta tayo kan inna tana zage zage da niyyar tureta,aikuwa tana sakin umman tasake tafiya rijib tazube aƙasa tasake ƙwallah ihu,ko waige Ikilima batayiba burinta ta ture inna wacce ke tsaye tana kallon yadda Ikilima ta zaburo kamar zatayi faɗa da Sa'arta, tana zuwa gaban inna taja ta tsaya kamar an riketa takasa tureta sbd wani irin kwarjini da taga innar tayi mata,dede lokacin kande ta fito daga ɗakin Amo tagama cika cikinta da fura.

Duk abinda ake tanajinsu, tana zuwa ta kwashe fuskar Ikilima da wani mari, tasa ƙafa fa kwashe kafar Ikilima tahau jibagarta sekace soja ya kama kwarto,ihu Ikilima keyi da kururuwa itada ummanta,sunata aikawa kande zagi da jafa'i kala2.

Ihunsu ya janyo hankalin sauran ƴan gidan aka firfito ana kallon wnn dramar,aka rasa wanda ze kwaci Ikilima a hannun kande,seda tanata lilis sannan ta kyaleta,inna kuwa aikinsa taci gaba da yi kamar bata gurin,kande tana gama jibgar Ikilima tasa kai tayi hanyar waje tana buɗa kafaɗa da hura hanci.

Seda ta fice sannan aka fara cece kuce, ana mayarda yadda akayi,umma se kururuwar ankashe mata ƴa take,tana jifan kande da munanan alkaba'i.

Amo kakar su kande tana ɗaki tana kallo batasan ma me ake ciki agidan ba, kasancewarta

bebiya ce,se akusa cinnawa gidan wuta da bala'i batasan anayiba. Kallon da takeyima in za a kasheta batasan me ake cewa ba,sede tayi ƙuru da ido tana kallon hoto tunda bajin abinda ake faɗa take ba.

Wai wacece kande ne.

_Ina masoyan MOMSANI ina wanda suka daɗe suna jiran wnn zazzafar tafiyar ta labarin kANDE,zaa kanwar maza,zaa soja,zaa kAND,to albishirinku yaude Allah ya nufa kuma yakawomu acikin wnn daddaɗan labarin me suna kANDE,bakijiba ne nace kANDE zaa tomboy_

_shin dake akayi daddaɗar tafiyar nan ta labarin Asma'u da Muhammad  Mahii ,SAURAYIN YAYATA,kin karanta labarin SIRIKATA,ko a'a,to albishirinku yauma momsani tasake dawo muku da wani daddaɗan labarin me dogon zango wato kANDE THE TOMBOY,in Sha Allah hajiyata bazakiyi nadamar karanta wnn labarinba_

_zazzafar tafiyace me ɗauke da zazzafan darasi,tare da nishadi,haɗi da ban tausayi,tattareda zazzafar soyayya,gamida cin amana dakuma butulci,bazan cika baki ba,bakuma zan cikaku da surutu ba,amma in Sha Allah karki bari ayi wannan mysterious journey din batare dakeba_

*kANDE littafin kuɗi ne akan farashi me sauki, Naira ₦400 kacal,idan kin shirya ki tura kudinki fa wnn asusun0591819457 SADIKA IBRAHIM gt bank,seku tura shedar biya ta wnn layin 07088282153,se na jiku masoya,i promise u will never regret*

Magoya ƴan amana Sena jiku,mom sani tana jiran ganin kauna daga gareku,love you all😘

Share fisabilillahi 🤲

🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Free page:02

Bismillahirrah manirrahim.

Mlm Hamza shine sunan mahaifin malam habu me kayan koli mahaifin kande,yanada mata biyu Amina da Hafsatu, Amina (Amo)itace uwar gidansa ta Daɗe bata haihuba har seda mlm Hamza yakara aure ya auro ƴar uwarsa Hafsatu ta haifi yaro namiji ana cemasa Musa,ko shekara beyiba Allah ya baiwa Amina ciki, tahaifi namiji itama aka sanya masa Abubakar, shekarar sa biyar Hafsatu takara haihuwar namiji aka sanya masa Mudassir.

Suna zamansu lfy daga baya Amina tafara wani irin ciwon kai da kunne harya kai tana ficewa a hayyacinta,idan ciwon ya taso seyayi kwana uku batasan inda kanta yake ba,anje asibiti sun kasa gano ainahin meyake damunta,haka aka koma na Hausa duk de bata canza zani ba,dg baya tafara wasu ƙuraje ajikinta kamar ƴan zufa, daga baya aka gane ashe baƙon dauro ne yakamata, duk da cewa bashida alaƙa da ciwon kanta,amma tunda aka gano baƙon dauro ne aka tashi tsaye da magani,daga wnn ciwon seya zamto batajin magana sosai,bakinta ma dakyar idan tayi magana ake gane abinda take faɗa,tun ana zuwa asibiti abu yaƙi sauki har daga baya idonta ma ya fara wani fari2,seya zamto bataji,bata gani,bata magana,hakan yasa tabar wasiyyar riƙon Abubakar a hannun Hafsatu,dan ta sakawa ranta ciwon bana tashi bane,iyayen Amina sunso su ɗauketa amma nlm Hamza da Hafsatu suka hana,Hafsatu na iya bakin ƙoƙarinta da Amina,mlm Hamza yana kan neman magani baya gajiya,cikin hukuncin Ubangiji aka kwatanta musu wani me maganin gargajiya hardana iska acen kura,datemakon Allah aka fara samun sauki,idonta ya washe haka tafara magana amma da ƙarfi,kunnenta yafara budewa ta yadda sekayi magana da karfi sannan zataji.

Wannan shine dalilin zamowar Amina bebiya,daga baƙon dauro takoma bebiya,bayan tasamu sauki sukaci gaba da zamansu da Hafsatu lafiya har lokacin kuma Abubakar na hannun Hafsatu ta haɗa da ƴaƴanta ta rike.

Kwatsam aka wayi gari Hafsatu ta rasu ba ciwo ba komi,daga baccin dare bata farka ba, Amina da mlm Hamza sunyi matukar yin baƙin cikin rashin Hafsatu daga baya suka dangana,se rikon yaran duka yakoma hannun Amina wacce suke kira da Amo.

Musa, Abubakar, Mudassir sun kasance ƴan uwa masu son junansu,sunada hadin kai sosai,sam bazakace suɗin ƴan uba bane,saboda suna da haɗin kai,manoma ne kamar mahaifinsu, suna noma da kiwo sosai hakan yasa sukeda rufin asiri sosai.

Sunyi karatu boko zuwa matakin secondary,daganan Abubakar yakoma cikin kasuwar ƴan kaba yana sana'ar hatsi da kayan lambu da kayan koli,Allah yasanya masa albarka aciki,Abubakar wanda akasuwa ake kiransa da mlm habu me kayan koli yanada tarin ilimin addini,ɗan izalane na gaske,hakan yasa da dare yake koyarda magidanta harma da samari agida,da karancin shekarunsa aka basa limami.

Shida ƴan uwansa suka sake gyare gidansu suka mayar dashi sashe huɗu inda kowansu yayi aure,aka barwa Amo da mlm Hamza shashe ɗaya,mlm habu duk yafi ƴan uwansa hali,hakan yasa yake temaka musu sosai,duk rabin ɗawainiyar gidan shine,sbd mahaifinsu yanzu baya aikin komi, zaune yake agida sbd jikin girma,sun bude masa shagon hatsi anan cikin unguwa,baya zuwa ko ina kullum yana shago kusada gida.

Matar mlm habu me suna A'isha mace ce me kirki da faram2,amma masifaffiyace sosai ta gaske inde aka shiga harkarta to ba mutunci,tanada kyauta sam bata da munafunci da shiga abinda be shafeta ba, itace ta fara haihuwa acikin gidan ta haifi namiji aka sanya masa sunan mlm Hamza,akwai kishin sauri sosai tsakaninta da matan su Hamza da Mudassir,sam basa sonta sun haɗe mata kai,kullum cikin zuga mazansu suke akan sun zauna basuda ƙwaƙƙaran aiki se noma,gashinan habu ya amshe girma da ragamar komi,sugasu su biyu shikuma shikaɗai amma yafisu arziki,akan haka Musa yataɓa sakin matarsa Zabba'u, wacce takasance sumumu kasau, batada hayaniya sam amma muguwa ce,ko alama bazata nuna fushi ko ɓacin rai afuskarta ba amma seta bada mamaki ta hanyar abinda zata aikata,batada mutunci,amma sam ba a ganewa,tunda aka mata saki ɗaya sbd iyalan mlm habu dashi kansa daga nan seta cenza takunta, ganin faɗan zahiri ba riba seta koma yi ta bayan fage.

Seta zuga matar Mudassir Hadiza,dake ita Allah yamata bakin tsiya,batada kunya ko

kaɗan,idan faɗa yahado ku duk abinda ya fito abakinta faɗa take yi kanta tsaye,sam bata ganin girman A'isha,ta tsani A'isha ga jan faɗan tsiya duk yadda ka kaiga hkr seta ƙureka ka tanka ta.

Hakan yabaiwa Zabba'u damar aiwatar da yaƙinta ta hanyar Hadiza.

Abangaren Mudassir tun baya ɗaukar zigar matarsa Hadiza hartaci galaba akansa ya fara adawa da ɗan uwansa,sam baya ganin ƙoƙarin mlm habu akansu.

Gashi su har lokacin Allah be basu ƴaƴa ba,seda A'isha ta haifi maza shida ajere, sannan haihuwa ta tsaya mata,Hamza,Hamis, Ibrahim, Musa, Mudassir,dan sefa yayiwa ƴan uwansa takwara sannan Aminu,bayan Hadiza matar Mudassir tasaka an riƙe bakin mahaifar A'isha ta hanyar asiri acewarta dan ita komi nata ba sirri,idan ranta yaɓaci seta furta mugun alkaba'i tare da cewa mutum seya gani,hakance ta kasance tacewa A'isha seta gani akan sunyi faɗa ranar sunan Aminu.

Alokacin ne kuma matar Musa ta haifi mace aka samata sunan Hafsatu,wata shida tsakani Hadiza ta haifi mace itama,Musa yayi2 da Mudassir yasaka sunan Amina amma ƴaki,sbd Hadiza tace muddin ya yarda aka sakawa ƴarta sunan amo to sede ya saketa kuma ba inda zata da ƴar sede ya kaiwa Amo bebiya da akayiwa takwara ta shayar da ita,shikuwa ba wacce yake ƙauna aduniya bayan Hadiza da ƴarsa,haka aka sanya wa yarinyar suna Hulera sunan uwar Hadiza kenan.

Alokacin ne mlm habu yarasu yayi ciwon kwana biyu yarasu.

Kwatsam Sega A'isha da ciki,hakan ya firgita Hadiza matuƙa dan tayi tunanin A'isha tagama haihuwa,a tunaninta A'isha bazata kuma haihuwa ba har ta mutu,hakan yasa ta sakankance kawai sede suka farga da tsohon ciki ajikin A'isha,haka tasake haihuwar ƴan biyu maza, alokacin ne akayi tashin hankali dan kiri kiri su Hadiza suka nuna baƙin cikinsu afili wai da gangan take haihuwar maza sbd ta cinye dukiyar gidan, alokacin ne suka raba gari tadena mu'amala dasu kwata2 bayan ta sauke musu kwandon hauka da shika-shikan rashin mutunci,dan ƴan uwanta masifaffu ne suma haka akayi baram baram,sam malam habu bayajin daɗin wnn rashin jituwar ta matansu,daga lokacin A'isha bata shiga harkar kowa acikin su,sbd akan fuskarta suka fada mata basa ƙaunarta itada mijinta da ƴaƴanta kuma in Allah ya yarda seta gani,hakan yasa ta tayarda bala'i sede mlm habu ya cenza mata gida sbd abinda facalolinta sukace, shikuma yace bame rabashi da ƴan uwansa, duk abinda yasamesa ko ƴaransa daga Allah ne bawanda ya isa ya cutar dasu se abinda Allah ya tsara masa.

Dama shine yake taka mata birki take rage wani abun,amma dan ta ita kullum se anyi bala'i agidan,ƙiri ƙiri se a dokar mata yara amma mlm habu yahata magana,ranar da ƴan biyu suka

rarrafa sukaje sashin mama suka zubar mata da gasara kashesu ne kawai Hadiza batayiba, dake tana sashen itama, A'isha na sallah sede ta dinga jin ihunsu ga ƙarar duka alamar dukansu ake,tana zuwa mama dake bakin ƙofar shashen tashige toilet da sauri, Hadiza ko bataga zuwan A'isha ba tayi nisa se zabga musu tsintsiyar kwakwa take a hannu,aikuwa kamar walƙiya A'isha tayi wani irin tafiyar yaji da Hadiza, duk kibarta seda A'isha ta kaita kasa tanata jibga, daƙyar aka raba wnn faɗan lokacin Hadiza tayi laushi se kuka take an fasa mata baki da hanci, se bayan anrabasu sannan mama tafito daga toilet tana sallallami, ko kallonta A'isha batayiba ta kwashi yaranta wanda suke ta ajiyar zuciya.

Aikuwa aranar Hadiza bata kwana agidan ba dan wani ƙaton macijine yashige ɗakinta kan gado ya fasa kai se huci yake.

Daga kan twins inna bata kuma haihuwa ba, kullum addu'ar ta Allah ya bata mace,tanason ƴa mace arayuwarta, gashi ba halin ta ɗauki yaran facalolinta yanzu se suce tanason ta kashe musu ƴaƴa.

Ahaka Zabba'u takara haihuwar mace aka sanya mata siddiqa se Maryam, Hadiza  kuwa bayan Hulera ta kara haihuwar Asiya, se Ikilima.

Mama kuwa daga baya Allah yabata namiji,kusan tare suka kara haihuwa da A'isha wacce batasan tanada cikiba har seda yayi girma ajikinta,bata faɗawa kowa ba segashi sun haihu tare da Zabba'u wacce yaran gidan suke kira da Mama,aranar Hadiza har suma takusa yi saboda baƙin ciki.

Zabba'u bata wani damuba ganin ta haifi namiji itama,amma sam aƙasan zuciyarta bataso A'isha wacce yara ke kira da inna tasake haihuwa ba,amma bakomi zasu gani,Hadiza de ita nata baƙin cikin afili yake amma bawanda yasan me mama take ciki tunda ita mijin nata yaƙi ɗaukar zuga.

Kasancewar inna a asibiti ta haihu wnn karon daga ita se mijinta, dan  ƴan uwanta ma seda aka sallamota sukaji haihuwar, ba wanda yasani har  uwar mijinta Amo hakan yasa seda suka dawo snn ƴan gidan sukasan ma haihuwa tayi kuma mace,ƴan uwan  A'isha ƴan bala'i ne basuda mutunci haka suka dinga kiɗe kiɗe suna shewa da guɗa an haifi kANDE,ranar suna yarinya taci suna Amina,anyiwa Amo takwara ba zaman Ify lols,seya kasance kamar ba suna biyu akeyi ba,ƴan uwan Aisha sun cika gida an kashe kuɗi anyi ɓarna sosai da kuɗi da abinci da nama, sam bazakace wai ana wani suna a sashen Zabba'u ba,dan da gayya ƴan uwan Aisha suke wani abun dan niyyar su ana tankasu se sun ci uwar mutum.

Wannan yaƙara girmama baƙin cikin Hadiza kuma taci alwashi sosai akan seta lalata rayuwar ahalin A'isha,inda mama Zabba'u ko ajikinta tunda de ta haifi namiji to ai angama komi,yaro yaci

suna Abdullahi.

Tare kande da Abdullahi suka taso se suka tashi kamar twins,  sam basaji ko kadan tare suke zuwa makaranta Arabic da boko kullum se ankawo kararsu ko sun daki yaran mutane ko sunyi wani abun,gasu da ƙoƙari amma sam basaji,kullum mlm habu na hanyar makarantar su,shekararsu biyar amma sam basaji,a lokacin umma takara haihuwa ta haifi Ikilima,daga lokacin se haihuwa ta tsaya musu duka matan gidan.

Kande irin yaran nan ne da ake kira  gifted, duk abinda aka karanta mata sau ɗaya yashige kanta kenan ba maimaici,nan take take ɗauke abu a kanta,tanada zuciya sosai batason reni,gata yarinya amma ƙoƙarin ta har tsoro yake baiwa inna da mlm, shekararta biyar amma tana iya karanta duk ayar da aka janyo acikin Kur'ani,sbd idan mlm habu na koyarwa a zaure itada Abdullahi suna gurinsa,hakan yasa duk yadda wasa ze dauke mata hankali baya hanata ɗauke abinda taji an karanta koda ba ita ake gayawa ba.

Kande ta tashi cikin tsananin soyayyar uwa da uba,ga yayye maza kowa kande, sunan da kakarta tasaka mata kenan Amo,itace take kiranta da kande ko kuma tace takwara,A'isha (inna) kuma tace uwar masu gida,wnn suna yana ƙonawa umma da mama rai,gabaki ɗaya sun tsani yarinyar ganin duka ƴan gidan kowa yana son kande, hatta ƴaƴansu ba wanda ya dakko baƙin halin uwarsa.

A cikin yaran Zabba'u siddiqa ita tafi kowa sanyi,yarinyar batada hayaniya sam,ga ilimin addini, baruwanta.

Yaran umma kuwa kusan dukkan su basu da hayaniya bakamar itaba,Ikilima ce kawai tayo halin uwarta.

Matan kusan duk sunyi aure, Hafsatu, Maryam,yaran Zabba'u duka sunyi aure, siddika ce kawai ta rage se Abdullahi autan mama.

Yaran umma ma Hulera da Asiya duk sunyi aure suma.

Kaf unguwar ansan gidansu kande gidane na ƴan izala masu ruko da addini,dan su Hamza daga malamin islamiyya se alaramma,se wanda ke kasuwa gurin kasuwanci,suka sunada aikin yinsu,bame zaman banza, twins kuwa suna jami'a.

Ko daga waje duk wanda ze shigo gidan to ina kande shine abinda ze furta,duk ta dusashe tauraron sauran yaran gidan,tun mama na damuwa harta gaji ta saki,umma ce kullum cikin

wahala, batada aiki se jifan kande da inna da mugayen alkaba'i,inde akan inna ne bata furta alheri.

Haka baba Musa komi ya samu kande,ko yace wnn na uwar masu gidane, Abdullahi ko kamar bashi ta haifeshiba ganin tasa tazo ɗaya da kande hakan yasa yaron ya tattare kayansa ya koma ɗakin inna.

Ankai ruwa rana sosai da mama, dan ta kafe akan ɗanta baze zauna agurin innaba, duk ƴaƴa maza da Allah yabata amma se ɗan gudalenta za a ɗauka awani baiwa inna,hakan yajanyo baba Musa yace idan takara tayarda zancen abakin aurenta,dan shi yana ƙaunar ɗan uwansa mlm habu,kuma sam baya ɗaukar wargi, hakan yasa baya iya hanasa ɗan uwansa  duk abinda ya nema,duk da cewa bashi ya nuna yanason ya rike Abdullahi ba amma ganin yaron nason zama agurin inna yasa yake jin nauyin amsarsa,dan gani yake kamar idan Abdullahi yabar gurin inna mlm habu zeji ba daɗi.

Mama tanaji gana gani aka rabaga da ɗanta,bata wani damu sosai ba dan tasan inna ba maƙetaciyar mutum bace,dan kular da ze samu agunta ko ita wacce ta haifeshi se haka.

Kwatsam wata rana aka baiwa kande scholarship daga makarantarsu zuwa babbar makarantar nan ta m.m. Haruna English academy, alokacin shekararta goma,tagama primary zataje secondary,dan jumping aka dinga yimata, ga haddar izu talatin akanta na Kur'ani.

Haka akayi ta murna agidan ana tayata farin ciki,inna kuwa har sadaka seda tayi.

Yayyenta maza kuwa kowa seda yabata kyauta.

Ranar ta ta farko a school.......

🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Free page:03

Bismillahirrah manirrahim.

Tun ranarta ta farko a makarantar tayi kawaye yaran masu kuɗi,tasaje da yaran masu kuɗi itama saboda irin kalarsu gareta,farace sosai,tanada tsayi ba lefi,gata da hanci da manyan ido,idan tana magana bakinta kamar bashi ke motsi ba,siraran lips ne da ita,fuskarta oval shape,sumar hanta tana da tsayi sosai,ga saje daya biyo ta gaban kunnen ta,tanda 1 side dimple, kyakkawar gaske ce,yarinyace amma jikinta a murje yake sosai,fatarta tanada matuqar kyau,snn gashin ta ba baƙi bane wuluk,akwai ruwan golden brown aciki hade da baƙi suffarta daban take kamar ba ɗiyar hausawa ba.

Ga ƙoƙari kamar alhuda-huda,komi aka fada mata sau daya ya zauna akanta kenan koda ba a ajinsu bane,hakan yasa satinta uku aka fara shirin yimata promotion zuwa j.s.s. 3,ranarda takoma gida tana murna tare da takaddar gayyata izuwa ha mlm habu,koda su umma sukaji labari nanfa bala'i ya tashi akan sede asaka Ikilima da saddiqa da Abdullahi a m.m. Haruna,duk da cewa siddika tana shekarar ƙarashe ne amma haka umma ta dinga bala'i,mama de uffan bata cewa,tagaji da yiwa inna hassada tunda kullum Sa'a a gefen inna da iyalanta yake.

Kwatsam rana tsaka aka dawo da kande dg school tafaɗi,sunkaita clinic na makaranta an dubata har drip ansaka mata amma sam taƙi ta farfaɗo,hankali tashe inna ta shinfiɗe ta,anata shafa mata ruwa taki farfaɗo wa, Amo kuwa banda ihun kuka ba abinda take,murya a sama irinta bebaye take faɗin,duk wanda yake son ganin bayan jikarta karya bari ta ganosa dan seta

yi masa rashin mutunci,haka taketa zabga bala'i tana ihu irin ta kurame.

Haka mlm habu yadawo ya samu autarsa unconscious,addu'a kawai yake tofa mata,haka ya karanta wasu manyan surori aruwa yace inna ta shafe mata jiki,yin hakan ko keda wuya ta farka,kamar robot haka ta miƙe tsaye batareda jikinta ya lanƙwashe ba,a tsorace inna ta matsa tana zare ido cike da faɗuwar gaba,duk yayyenta dake ɗakin ba wanda be tsorata ba ganin yanayin da ta farka aciki.

Fuskarta tayi kore sosai,jikinta ma haka,idonta yakoma ɓaki duka ko ƙwayar fari babu,cikin buɗaɗɗiyar murya kamar ta maza tace "lahuhu irmati gidigam gam,abukanwatur fadurma gim gam" kamar wata bokanya haka take furta wasu irin dalamisai,jikinta banda jijjiga ba abinda yake,bakinta har wani hayaƙi yake fitarwa, nan take dakin ya fara jijjiga kamar ze ruguje,cikin ɗaga murya mlm habu ya fara karatun suratul baƙara,yi yake da karfi, nan take su Hamza suka ɗauka,da karfi suke karatun, Amo na gefe se tsandara ihu take kamar ana yankata, ta tsula fitsari yakai sau biyar,sun rungume itada inna se kuka suke, Amo se ihu take tana gwalanci wai nan addu'a take.

Ihu kande tafara yi tana jijjiga kamar ba mutum ba,cen tayi wata irin gigitacciyar ƙara wacce duk maƙotansu seda sukaji,gashi marece ne anata kiraye-kirayen sallar magrib, ihu take tana susar jikinta kafin takara yanka wani ihu me karfin da yafi na baya tazube aƙasa ta zauna kamar ƴar bori, still su mlm habu basu dena karatunba sema wasu manyan ayoyi da suke sake janyo wa,kamar a mafarki tafara rera karatun tare dasu,idan suka cenza aya itama tacenza har suka yi shiru,amma ita seda takai ƙarshen aya.

Zuciyar mlm habu akarye cike da firgicin wannan sabon al'amari daya riskesu yau,amma Cikin dakiya ya buɗa muryarsa babu wasa yace "wanene kai? Me kake yi ajikin ƙanƙanuwar yarinya irin wnn? Ko ta yimaka wani laifin ne da ka zaɓi shiga cikin jikinta,kuma ga dukka alamu sun nuna cewa kai ɗin musulmi ne".

Cikin wata babbar murya marar hayaniya akace "Assalamu alaika ya Imam Abubakar bin Hamza,Tabbas ni muslumi ne kamar yadda kaji,kuma sunana Muhammad Arun ɗan Sarkin aljanun baihak,ni musulmi ne,kuma ni ɗin na kasance ajikinta tun tana cikin cikin mahaifiyarta,sannan ni ne wanda nake bata kariya bisa umarnin kakana muzgar".

Jikin inna da Amo banda rawa ba abinda yake,yayyenta ma dauriya kawai suke,domin abin babu daɗin gani kwata kwata halittar jikinta ya sauya kamar wani ƙaton gardi, ga wasu jijiyoyi sun ratsa mata a damtsen hannunta,gashi daga ita se vest da leggins.

Jinjina kai Malam habu ya yi yace "tabbas nagani kuma naji kai ɗin musulmi ne,amma shin me

wannan yarinya ta aika maka,ko ta cutar da kai ne dayasa ka bayyana akanta ko kuwa?".

"Babu ɗaya daga cikin biyun tambayoyin ka,wato zancen gsky naso nayi zamana shiru batareda na nuna wata alamar cewa ina tare da itaba,amma hakan baze taɓa yiyuwa ba,anyiwa goɗiya wani mummunar sihiri wanda akaso bayan tagama wulaqanta tayi mummunar mutuwa. An sadaukar da jini ga baƙaƙen aljanu an tura su jikinta da mummunar niyya,kuwa hakan yakusa yin tasiri sakamakon bama tare da ita a lokacin ,munyi wata doguwar tafiya zuwa ƙasar misra domin gabatar da wani yaƙi acen tsibirin asgarul mundal, sannan mun nasaka fararen rauhanai a domin bata kariya da kuma gadinta kafin mu dawo,amma se akayi rashin Sa'a baƙaƙen aljanun da aka turawa goɗiya sunfi ƙarfinsu,hakan yasa sukayi nasara akansu har suka raunatasu,duk da cewa mun  bar wani kariya ajikinta hakan yasa sukayi kwanaki bakwai suna fama kafin su sami nasarar shiga jikinta ta hanyar wacce tayi mata turensu,tabata ɗan wake taci,acikin ɗanwaken akwai wani magani wanda ya karya garkuwar da muka bari atareda ita,a jiya ne muka sami nasara akan baƙaƙen aljanun da suka addabi tsibirin da mukaje yaƙi,cike da azama muka dawo gareta kwatsam se mukayi arba da shugaban baƙaƙen aljanun da muka nema muka rasa a fagen yaƙi, yana shirin ɗaukar rayuwar goɗiyarmu,wanda da hakan ta kasance to tabbas da sede mu mutu atare da ita, domin rayuwar mu gaba ɗaya sadaukarwa ce ga ahalin goɗiya.

Kakan goɗiya ya taba temakon kakana alokacin da yayi ɓadda kama amatsayin ɗan Adam kuma almajiri, lokacin kakana ba musulmi bane,amma karamcin da kakanta yayi masa yataɓa zuciyarsa,har ya amshi musulunci,a dalilin haka yasa yake bibiyar ahalinsu.

kakanta ya temaki kakanmu,  yana saurayi a lokacin batareda ma yasan cewa aljani yatemaka wa ba,a hannun kakanta Abu Rayyan kakana ya amshi musulunci,hakan yasa kakana ya tara iyayenmu yabasu labari kuma ya umurce su da amsar musulunci tare da faɗa musu lalle su kasance masu baiwa ahalin Abu Rayyan kariya har ƙarshen rayuwarsu.

Mun kasance tare da mahaifin goɗiya kafin faruwar wani babban al'amari, daga baya kuma muka koma gareta tun acikin cikin mahaifiyarta,.

Tabbas makashinku na tare daku, tabbas anaso a salwantar da rayuwar goɗiyarmu hakan yasa muka riƙe baƙin aljani Gandamul arzu bawai dan bazamu iya galaba akansa ba, a'a sedan munaso ya bayyana ajikinta akan idon ku,yaso tserewa tun da sa'ar da mukayi arba da juna aɗazu,amma na riƙesa sakamakon munaso kufara hukunta sa da kanku da ayoyin Allah,ya yi iya yinsa dan ganin be iso nan ba,sbd yasan karonsa da mlm ba zeyi masa kyau ba amma sam bamu basa damar yin hakan ba.
Niyyarsa ya aiwatar da abinda aka aikosa yakama gabansa batareda ya iso gidan nan ba amma bamu basa damar guduwa ba.

Shine wanda ya fara bayyana ajikinta sakamakon ruwan addu'a da aka shafa mata, seda muka tabbatar kun ƙonasa da ayoyin Allah ta yadda baze ƙara moruwa ba kafin muka barsa ya fita,fita ta har abada bakuma ze ƙara gigin shafarta ba".

Se yanzu ta sauke numfashi idanunta arufe,cikin sanyin jiki malam yace in Sha Allah babu abinda wani mahaluki ya isa ya yi agaremu face abinda Allah ya tsara mana.

Tabbas munji daɗi kuma muna gdy bisa kariyar da ka kasance kana baiwa ƴarmu,amma kasani mudin bil adama ne babu wani haɗi tsakanin mu daku, muna godiya matuqa amma dole zaka bar jikin wnn yarinya,idan kayi duba da ƙarancin shekarunta sbd haka ina gamaka da Allah akan kayi haƙuri ka barta".

Ido rufe kuma cikin wata murya wacce ta fi ta farko ƙarfi da firgitarwa tace "wannan ne kuma bazamu iya yi muku alqawarin aikatawa ba,zamu tafi yanzu,bazamu kuma bayyana ba,kuma zamu ɗauki mataki dede gwargwadon abinda aka aikata wa goɗiyar mu,sannan zamu aikata wani al'amari atareda goɗiya wanda muka tabbatar shine kariya agareta kuma zaman lafiyar kowa aciki harda ku,duk abinda zata aikata kar wanda ya ƙalubalanceta akai,tabbas komi yanada lokacinsa, kuma idan lokacin da muka dibarwa hukuncin da zamu yanke ya kai to tabbas komi ze bayyana.

Mlm Abubakar bin Hamza tabbas kaiɗin mutumin kirki ne,ka kasance me aikata alheri akoda yaushe,kuma me saka sharri da alheri,saboda haka karka ce zaka ɗauki wani mataki akan hukuncin mu,zamu tafiiii amma kusani muna tare da goɗiya akoda yaushe,domin nauyin kare ta yana rataye a wuyan ahalinmu,wannan alƙawarine.

NATAFIIIIIII...., KUMA ZAN DAWOOO...."

Wata babbar hamma kande tayi kafin ta tafi yaraf ta kwanta kamar ta mutu, wani nannauyan bacci ne ya yi awon gaba da ita.

A lokacin sallar isha'i ake kira,jikin malam habu amatuqar sanyaye yatashi tasake tofe kande ta addu'o'i,wacce banda gumi ba abinda take,dukama wanda yake ɗakin ya haɗa uwar zufa.

Se a sannan inna da Amo wanda idonsu yajiƙe sharkaf da hawaye ya kumbura suka saki junansu,kaka Amo kamar abin tsafi duk abinda ya wakana taji raɗau kamar ba bebiya ba.

Zuciyoyin duka wanda suke cikin ɗakin ɗauke da tambayoyi masu yawa amma kowa ya bari har lokacin daya dace kafin ya furta.

Haka mazan suka fito daga ɗakin jiki a sanyaye,akan idon mlm habu yaga gittawar mutum da gudu ya yi hanyar waje.

Girgiza Kai kawai mlm habu ya yi dan sarai ya gane ko wanene,kawai shiri ya yi,kuma yasawa ransa koma menene da yaddar Allah baza ayi nasara akansu ba.

Haka kande ta share kwana biyu batasan inda kanta yake ba,kullum se malam yamata tofi aruwa ashafe mata jiki.

Yau kamar a mafarki inna tana sallar azahar taga wani abu kamar inuwar mutum ya tsaya adede kan kande.

🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Free page:04

Bismillahirrah manirrahim.

Kafin inna ta karasa setaga kamar wannan inuwar ta faɗa ajikin kanden.

Saurin miƙewa tayi bakinta ɗauke da addu'o'i ta nufo inda kanden take akwance,tana zuwa dede lokacin kande ta buɗe idonta wanda sukayi jajir jini ya kwanta acikinsu kamar an zuba mata,baka ganin farin cikin idon ko kaɗan,tana gani tar amma idon yayi mata nauyi.

"Alhamdulillah" shine abinda inna ta furta tana kama hannun kanden datake miƙa mata.

Jikinta yayi mata nauyi sosai bata iya motsa ko ɗan yatsan ta,kuka inna keyi ƙasa ƙasa,ta janyo wayarta keypad tana dannanwa mlm habu kira, alokacin shi kuma ya shigo cikin gidan hannunsa ɗauke da wata gora ta ruwan addu'a, Kasancewar an idar da sallar ya sallami ɗalibansa masu ɗaukar karatu,tare suka shigo da twins wanda suka dawo sbd ciwon kanden.

Dasauri mlm habu yakarasa shiga ɗakin yana tofa mata addu'o'i,ahankali yace "mamana", bakinta yamata nauyi sosai amma ta ɗaga idon ta wanda yake nan gwanin tsoro sbd yadda ya koma ta kallesa,hakan yabashi tabbacin ta dawo cikin hankalinta,

Sake tausasa murya ya yi bayan ya janyota daga kwance ya mayar jikinsa ta jingine dashi ya sake cewa "kingane wacece wnn?" Yafada yana nuna inna dake durƙushe kusada gadon tana hawaye,ganin yadda fuskar ƴar ta ta ya kumbura sosai bakinta abushe idonta babu daɗin kallo.

Jinjina kai tayi a hankali alamar ta ganeta, "waɗannan fa?" Ya nuna su twins wanda suma hawayen suke,dan akwai shaƙuwa me tsanani tsakaninta dasu kamar ba saƙonnin ta ba,duk ma yayyen ta maza suna matuƙar ƙaunarta,sake jinjina kai taji a hankali,amma ba magana.

Hamdala mlm da inna sukayi,gorar ruwan addu'a mlm ya ɗakko ya yi bismillah ya kafa mata gorar abaki,ba musu ta amsa ta fara sha da sauri, sefa tayi rabi kafin ya cire mata ta huta,sannan ya sake miko mata ta amsa seda ta shanye tas,kaɗan ta bari ya zubaa hannu ya shafa mata afuska sannan ya ajiye gorar.

Lumshe ido tayi tana sauke ajiyar zuciya kafin ta fara yinƙurin amai,da sauri inna ta miƙo mata wani ƙaramin baho aikuwa tafara sheqa wani irin amai baƙiƙirin dashi,harda wasu abubuwa

kamar kwalba, aman babu kyan gani,ga wasu abubuwa kamar tsutsa se motsi suke,seda takusa yin rabin bahon kafin aman ya tsaya mata,takoma jikin mlm tana sauke wani wahalallen numfashi,ba jimawa wani baccin ya sake kwasheta.

Shimfiɗeta mlm yayi yasake tofeta da addu'a kafin suka sake fita.

Seda takai la'asar tana bacci kafin ta farka,cikin ikon Allah koda ta farka idonta ya fara washewa kuma harta iya tashi da kanta ta zauna, Amo na gefe se zare ido take,dazarar taga kande zata kallo ta setayi maza ta ƙara damƙe carbin ta,murya asama take istigfari,dan wlh tsoron bala'i kanden ke bata,ganin take har yanzu al janun na nan basu tafi ba.

Inna ce tashigo ta kamata suka shiga toilet takai mata ruwan zafi wanda mlm ya yi mata tofi aciki,inna tayi mata wanka dan har lokacin jikinta babu ƙarfi.

Tea me kauri inna ta haɗa mata da ruwan addu'a wanda mlm ya yi mata shi dayawa komi nata inde naci ne ko nasha to da wnn ruwan za'ayi mata amfani,har wanka.

Duk wannan abin da ake yi umma bata leƙo sashen ba ko sau ɗaya,mama de ta shigo sau ɗaya ta tsaya daga bakin ƙofa tace Allah y kafa afuwa tayi gaba,ko takalma bata cireba balle tashi ɗakin.

Duk da inna taji zafin abinda suka mata amma taji daɗin yadda mama tazo ta duba jikin ƴarta,koba komi de tazo,tafi umma wacce ko bakin ƙofar sashen bata leƙo ba.

Seda kande ta shafe sati ɗaya kafin ta fara magana, maganar ma me ban mamaki dan kamar wata namiji haka take magana tana wani karkace baki gefe,da farko abin dariya ya baiwa inna hartana cewa "haba uwar masu gida,daga buɗe baki kuma se shegan taka,meye haka kamar namiji?" Tafaɗa tana murmushi.

Cikin cijewa kande tace "yo inna  da mecece ni ɗin,ai ni namijice kawai totally,kallifa duka yayyena maza ne" tafaɗa tana nuna su Hamza da su Hamis da twins dasuka kalli juna., saboda haka nima namiji ne kuma soja zan zama in Sha Allah.

Ya Musa yace "haba auta ke mace ce,kuma kyakkawar yarinya,ƴar autar inna da malam,jikar Amo kallifa ji sumarki me kyau da ita ga tsayi".

Kallonsa tayi tace "Allah ko ya Musa,wannan gashin shiya sake saka wa nake kama da mata ko? To yau base gobe ba zan askesa,Sena je an aske mini shi".

Kamar wasa tafara acting kamar namiji,duk kayan da inna ta ɗakko mata ta sanya setace sam bata sonshi, ita sede anemo mata riga da wando su zata saka.

Tun Inna na kallon abun a matsayin wasa har tafara jin haushi,cikin fusata tace "zanci ubanki fa,ki tashi ki saka kayanki,tun ɗazu kin sauna da ɗaurin zani,karki bari raina ya ɓaci", se mafifa inna take.

Nan take idon kande ya cenza tayi tsaye ƙiƙam taki motsi ta sunkuyar da kanta gashinta ya zubo ya rufe mata fuska,inna tayi magana har ta gaji amma shiru babu amsa,ganin hakan yasa ta sakko ta fara lallashi da ban baki,amma shiru kamar tanayi da dutse.

Matsowa inna tayi ta dafa kande tana yimata waƙa kamar yadda take mata idan tayi fushi, amma ko alamar zata motsa babu,janyota inna tayi da niyyar rungumeta amma taƙi janyu wa,sema ji tayi kamar ba mutum take jaba, kamar gini haka ta maƙale agurin, cikin tsoro inna ta saketa taja da baya,aguje ta ruga zuwa zauren gidan tana ƙwalawa mlm kira, jikinta banda rawa ba abinda yake.

Arikice ta fada zauren inda mlm ke tsakiyar karatu da ɗalibansa,da sauri ya tashi yana tarota,cikin sauri kuma ya janye ta sukayi cikin gidan yana tambayar ta meya sameta harya firgita ta  haka,inna banda rawa ba abinda jikinta yake se nuna masa hanyar ɗakinta take,ta kasa magana hawaye se zuriya yake akan fuskarta.

Hanyar ɗakin ya nufa da ita,amma ta cije a waje taki shiga,baiwar Allah Inna banda rawa ba abinda jikinta yake.

Sakinta mlm ya yi yashiga ɗakin yaga kande a halin da take,bakinsa ɗauke da addu'a yake nufarta,haka mlm ya shafe tsawon lokaci aɗakin kafin ya fito yana sharce gumi.

Yana fitowa Sega kande abayansa tana faɗin "inna yunwa nake ji wallahi,dan Allah kiyi mana ɗan wake", jikin inna be dena rawa ba ta kalli malam,jinjina mata kai ya yi alamar bamatsala.

Cikin ɗari2 inna tace "to auta in Sha Allah,zoki amso mana fulawar", inna ta fada tana miƙo mata naira dubun da mlm ya bayar,cikin murna ta yi hanyar waje daga ita se ɗaurin zani a ƙirji ko ɗan kwali babu akanta,ga dogon two color hair dinta dakenan har kusada mazaunanta yanata tashi iska na kaɗa mata shi,kamar ba ƴar hausawa ba,da sauri mlm yace "a'a uwata kawo na bayar a amso muku", haka tundaga wannan ranar kande ta koma me siffar maza.

Bawai jikinta bane ya koma siffar mazan, a'a,tana nan a yadda take,kawai de gabaki ɗaya yadda take gudanar da al'amaran rayuwarta ne ya koma na maza,inna batasan ya akayi ba se ganin kan kande tayi an aske mata rabin sumarta, normally sumarta ta kai har ɗuwawu amma kawai se wayar gari akayi an yanke Mata fiye da rabi yakoma kamar na namijin ba indiye.

Shigarta da komi nata sak namiji, school ma ta dena zuwa,ɗan karatun ta da ake taƙama dashi aka nemeshi aka rasa,bayan fatiha babu abinda kande ke karanta wa daidai,a fannin boko kuwa ɗum,kai ya koma kamar na kifi bata gane komi,tunrancin da yazamewa bakinta kamar yaren ta na usuli shima aka nemesa aka rasa,komi nata kamar an juya mata shi,tamkar yadda ake juya riga daga Dede takoma baibai.

Ada ta kasance me yawan son turanci,har bayan samun matsalar ma bata dena son yin turanci ba,amma fa kafurin broken english take kwaɓawa,baƙaramin ciwa turanci zarafi take ba,idan ta kwaɓa wani turancin se dariya ta kusa kashe mutum,amma ita ko ajikinta,ta fuske,ita adole turancin gaske take.

Ga baki daya rayuwarta tayi juyin waina acikin tanda,yayyenta maza abun ya yi musu ciwo sosai,gashi sun kasa samun wata gamsashshiyar amsa daga iyayen nasu,sude sun san tun sa'adda tasamu matsalar jinnu din nan bata kuma samun kanta ba,kullum da abinda zata fitar sabo arayuwarta.

Tun ranarda sukayi ƙungiya sukayiwa inna ƴar tsure tare da jefa mata wata nannauyar tmby wanda yakusa zautar da jin ta,har girgizar da tayi sanadiyar tambayar su ya bayyana afili,nan take ta fatattakesu sbd rashin gamsashshiyar amsar da zata baiwa ƴaƴan nata.

Hakan yasa suka juya tmbyr izuwa kan mlm,tabbas shima ba ƙaramin jijjigashi tambayar tayi ba,amma dayake namijin gaske ne shi be nuna ya firgita da tmbyr ba.

Cikin dakiya mlm yace "Hamza me kace?,me kuke son sani gameda lalurar ƴar uwarku ne?bayan komi akan idon ku ya faru,kuma duk abinda aljanin yafada kunji da kunnenku".

Maimaita tambayar Hamis ya yi cikin kwantar da murya yace "am mlm dama cewa

mukayi,menene gaskiya akan abinda muka ji aljanin kan auta ya faɗi?shin wanene Abu Rayyan,menene dalilin da ya sanya gabaki ɗaya rayuwar auta ya cenza,kuma munga baka ɗauki kowanne mataki ba,kamar ma abinda take yi yanzu baya damunka,gashi mutanen unguwa harsun fara gutsira zantuttuka akan sabon tsarin rayuwar da ta ɗakko a yanzu,sam sekace ba ƴarka ba,komi nata ya sauya,mlm dubi yadda takoma sak namiji,kuma ma dakanka ne kabata kuɗi tasai irin tufafin da maza suke sakawa,wanda kaine ka koyar damu cewa duk namijin da yake kamanceceniya da mata to yanada babban zunubi agurin Allah (s.w.a),haka ma ga macen ta take kamanceceniya da maza,harfa yanke gashin kanta tayi,wanda yin hakan a addini shima haram ne,gashi yanzu bata tsoron kowa,shekaran jiya nan naga ta kama Ikilima tamata shegen duka seda ta yimata targaɗe a hannu,mlm dan Allah kafaɗa mana menene asalin abinda yake faruwa wanda mu bamu sanshi ba,kuma wanene ABU RAYYAN* a iya sanin mu kune iyayenmu,kuma aduk cikin kakanni mu bamusan wani me suna abu Rayyan ba,mlm kai masani ne wanda Allah yabashi baiwar ilimummuka me tarin yawa,kuma abinda take yi Sam ko a addini be dace ba,idan ma sbd aljanun kanta ne ai Allah ya baka sani ta yadda zaka magance komi batareda an bar wani aljani ya sauya mata rayuwarta hakaba,ka gafarcemi mlm idan na faɗi abinda ya sosa maka rai,bada nufi bane ".

Dogon numfashi mlm yaja kafin yace "duk naji abubuwan da ka faɗa kuma tabbas maganganun ka gaskiya ne,amma abunda nakeson ka sani,duk wata cuta Allah be halicce ta ba har seda ya fara saukar da maganinta, sannan idan ka lura gaba ɗaya rayuwar auta maƙiya ne a kewaye da ita wanda nasani kuma kun sani,tun kafin bayyanar wannan aljanin atare da ita ansha neman nakasta rayuwarta wanda ku ƙila a yau kuka san wannan,akwai aljanun da zaman su atareda mu bil adama babu alheri wanda hakan kesa muke yin duk yadda zamuyi araba wanda suka shafa dasu,akwai kuma nau'in aljanun da zaman su atareda mu wata kariya ce daga Ubangiji*

Tabbas rayuwar auta ta sauya kuma babu wani wanda hakan kewa daɗi daga Ni har mahaifiyarku,kuma duk yadda zakuji ciwon sauyawarta baku kai mu ba tunda mune muka kawota duniya,kuyi hakuri kubata lokaci,idan kun lura harda kuruciya a lamarin uwata,in Sha Allah komi ze dedeta da izinin Allah*

Ni nasan abunda baku saniba,wanda in Sha Allah idan lokacin kusani ya yi tabbas ba makawa se kun sanshi,rayuwar auta akwai wasu manyan sirrika wanda lokaci ze bayyana su,kuyi hakuri ku bata lokaci,kuma ina roƙon ku kar wanda ya hanata abinda take ko ta nema,inde befi ƙarfin ku ba ina neman alfarma abata,sannan Abu Rayyan bakowa bane kawai zancen aljanin ne,nagama magana kutashi kuje Allah ya yi muku albarka".

Sam mlm be basu damar yin wata magana ba,kuma tabbas sunajin cewa akwai abinda mlm be faɗa musu ba,amma kamar yadda yace komi lokacine suna fatar lokacin nan ba anesa yake ba,dan duk wanda yasan auta ada yarinya me hankali ga ƙoƙari ga son karatu,to ba ze yadda itace ta koma yadda take a yanzu ba,yarinya ƙarama me shekaru goma zuwa sha ɗaya,sam kamanninta ya sauya,babu wata cikakkiyar nutsuwa atare da ita,ga rashin kunya,duk wani ilimi da take dashi yanzu babu ya gudu,takoma kamar jaka, bata da mutunci sam,ga ƙarfi kamar ba

mutum ba,ba wanda ya isa ya ɗaga mata yatsa ko ya ɗagawa innarta,duk mutanen gidan yanzu shakkar ta ake, ƙaramar yarinya amma ta addabi kowa,musamman umma da ƴarta Ikilima wanda suke nuna sam basuda alaƙa da ita,mama de dama ba shiga shirgin kande take ba,tun bayan da ɗanta Abdullahi yakoma sashen ta shikenan burinta ya cika,dama ba dan Allah ya barshi a gurin inna ba, barazanar da mlm Musa mijinta yamata ne yasanya ta kyaleshi acen,amma yanzu tunda ya dawo gurinta ba abinda ya shalleta dasu.

Fuskarsa da kansa  dake da farin gashi ne kawai yake nuna ya manyan ta amma jikinsa amurje yake kamar matashi, yanada kyau sosai,jikinsa sanyeda wata irin suit se walwali take kamar an shafa mata gold,yana zaune agaban wani babban teburi aɗakin taro,kallon Dr Joshi  ya yi yasaki wani wild smirk yace cikin harshen indianci "idan kana buƙatar ƴarka ta dawo gida safe nd sound dolene ka yarda da deal ɗin da muka kawo maka,dole ne kayi mana gwajin magungunan mu akan mata masu juna biyu,dole kuma duk cikin da yakai wata biyar kasan yadda kayi ya lalace domin wannan jinin miscarriage ɗin muke da buƙata a tara mana,idan kayi hakan ina me tabbatar maka seka zama shararren me kuɗin da duk fadin india babu me irinsa,namaka alkawarin wannan,sannan zan saka asibitin ka yazama lamba ɗaya da duk duniya zata san da zamansa,kaide kawai kabi sharaɗin da zamu gindaya maka,ina binka da lalama ne kawai saboda ƙwarewarka a aiki shine jarinda nakeson amfani dashi a wannan harƙallar,amma ba dan hakaba da kota ƙarfi Sena saka kayi abinda nake da buƙatarka".

Banda gumi ba abinda yake zuba ajikin Dr Joshi,Amma ba yadda ya iya inde yana buƙatar zaman lafiyar iyalansa dole ya aikata abinda suka so.

Yana cikin wannan tunanin wasu manyan manyan mutane suka shigo sanyeda kayan likitoci suka ajiye masa wasu akwatuna suka juya suka fice.

Kallon wayar yayi inda yaji ana masa magana "wannan sune allurorin na baƙin case sune muke buƙatar ka gwada su akan duk wata me tsohon ciki,su kuma na jan case din sune magungunan da zakana basu suna sha,se farin case suma allurai ne,duk macen da ka tabbatar cikinta ya kai wata biyar ko shida to akansu ne zaka yi amfani da wannan allurar,sannan zamu riƙe ƴarka dake gurin mu,har seka aiwatar da aikinmu na tsawon shekaru daya kafin musaketa" kafin ya yi wata magana sukayi saurin disconnect na kiran bisa umurnin na cikin babban screen din wanda ko sunan sa Dr Joshi be sani ba.

Wani irin kuka Dr Joshi keyi,ƴar sa shekararta goma sha huɗu,yarinyace ƙarama kuma ita kaɗai yakeda,tabbas bayason ya rasata, haka kuma bayason aikata wannan mummunar aikin da suka sanya sa akan al'ummar da basu ji ba basu gani ba,sbd yasan allurorin yasan haɗarin su.

Su wadanda akace ya yiwa masu tsohon ciki illarta shine zata sakarwa jaririn cikin cutar kansa me hadari,wanda zata iya illata har uwar ba wai yaron kadai ba,idan akayi babbar Sa'a shine za a haifi cikin amma baze zo da lfy ba, daganan se su kawo wani magani wanda shine maganin cutar wannan shine kasuwancin da suka kulla da asibitoci da dama a faɗin duniya,wani kuwa tun aciki yake mutuwa kokuma daga uwar har yaron su mutu,kuma se sun zaƙulo babban likita me cikakkiyar ƙwarewa da sanin kan aikinsa sannan suke kai masa wannan farmakin,duk kuma wanda ya bijire ko masa barazanar za akasheshi ko kuma akashe wani nasa da haka wasu suke yadda wasu kuma tayin farko idan sukaji maƙudan  kudade kai tsaye suke amincewa.

Ita kuma ta masu cikin wata biyar itace wacce zata lalata cikin har se an kwashe musu,to jini ɓarin ake siyarwa wasu kamfanoni masu yin mayukan fata dana bleaching,ba iya nan ba har matsafa suna siyarwa.

Haka Dr Joshi ya yanke shawarar kawai ya kashe kansa akan ya aikata wannan mummunar aikin da ɗaukar alhakin al'umma Gara kawai yakashe kansa,dan yasan ƴarsa dake gunsu ma ba zasu barta lfy ba,bama ze kuma ganinta ba,gara kawai yakashe kansa,wayarsa ya ɗauka ya yi video akan duk abinda ya faru da duk wani details akan harƙallar ya turawa wani abokinsa dake aiki a Dubai,ko minti biyar beyiba saƙo ya shigo wayarsa da sauri ya duba atunanin sa abokin nasa ne,amma se ganin wani vedio ya yi daya jijjiga duniyarsa.

<><><><><><><>

Kande tana tafiya amma jitake kamar ana binta idan ta waiwaya kuma bata ganin kowa,tun tana shiru harta ci birki tana faɗin "ko wane arne ne yake bin bayana kawai yayo waje na gansa,in ba hakaba zan ci me ɗumama masa tuwo Allah wlh" se mafita take ita kaɗai amma ba wanda ko gittawa ya yi a hanyar,cigaba tayi da tafiyarta ta nigogi tana masifa,amma still tanajin takun mutum alamar ana biye da ita,kamar bazata juyo ba tayi kamar bata damuba kawai ta juyo da sauri aikuwa idonta ya faɗa akan wannan mahaukacin yana dab da ita.

Cikin ɗan firgita da yadda ya ke dab da ita tace "kai kirezi dan fazaan ka kasha Omo ne iye, y are u follow me,are u mad?" Sekuma tace jini kuma ina tambayarasa bayan mahaukacin ne.

Daukar wata sanda tayi tace "ware kabar nan dan me dafa muku tuwo agidanku,bar nan kona maka ɗaukar amarya na jibga a ƙas" bawan Allah ganin ga ɗakko bulala ai aguje ya ruga ya

barta se Bala'i take ita kaɗai

Acen gida kuwa mama ce tazugo umma wai an hana ƴaƴanta su Hafsah haihuwa se cinye musu ciki ake tanata kuka,aikuwa umma dake ba hankali ne da itaba ta dinga yada magana acikin gida amma inna bata kulata ba sema ɗauko kwanon silbarta data zuba miyar da tayiwa Hafsatu tayi ta ajiye aƙasa tana kullo kofar sashen ta.

Umma ganin inna tamata banza cikin jin haushi tace "Allah wadaran maye me cinyewa mutane ƴaƴa" cikin zafin rai inna ta waiwayo ta kwashe fuskar umma da mari dede lokacin da Mudassir ya sanyo kai cikin gidan.

🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Not edited

Free page:09

Bismillahirrah manirrahim.

Salati Mudassir yasaki yana fizgo umma daga riƙon da inna ta mata se fyalla mata mari take,cikin ɓacin rai yace "yau base gobe ba zamu bar gidan nan,Ni dama na daɗe da sanin ba'a

son zamana da iyalina acikin gidan nan,kullum se  kande ta kama Ikilima ta daka,yau kuma abin yakoma kan matata to ni bazan ɗauka ba,maza Hadiza tafi ki fara harhaɗe mana kayan mu".

Turo baki gaba umma tayi tace "nide gsky wnn gidan ko wutafa baka ja mana ba,Allah ya gani ba zan iya kwana acikin zafi ba,Ikilima ma jikinta baya son sauro kasani"

Mama dake laɓe abayan ƙofar sashen ta tayi tsuki ganin faɗan beyi nisa ba takoma ɗaki.

Umma tuni tayi gaba tabarsu nan suna kayan haushinsu, itade ko gobe idan Hadiza zata dinga shiga hanyarta to baza ta gaji da gyara mata zama ba itama,a zaure ta haɗu da mlm habu wanda duk abinda ake yana jinsu,har abinda Hadiza tace yana ji, murmushi kawai ya yi don yasan ko sama da ƙasa zasu haɗe Hadiza bazata iya barin gidan nan ba,sallama inna ta masa yace mata adawo Ify yabata wani ruwa acikin gora guda biyu yace idan taje ta baiwa ko waccensu, in Sha Allah inde matsalarsu ba daga Allah bace shafar jinnu ce ko wani al'amari na Ubangiji to in Allah yaso bazasu kuma ɓarin ciki ba,dan idan be manta ba Hafsatu ɓari na biyar kenan tayi,ita kuma Maryam ɓarinta biyu wnn ne aketa murna harya kai wata biyar se kuma gashi naƙuda ta taso mata da alama shima ɓarinsa za'a yi.

Amsa inna tayi ta fice,a waje taga baba Musa tayi masa sallama ya tsare mata napep tana ya barshi amma seda ya biya me napep ɗin,yanata yi mata gdy da sa albarka itada mlm habu,dan duk sanda irin haka ta samu yaran nasa itace take ƙoƙari dasu,duk shirin umma da mama,mama bata bari umma taje gidan su Hafsatu ba wanda yasan dalilinta,ita ma umman bata sani ba,ko a kwalar rigarta ma abin baya damunta dan ita ba mutum bace me son zuwa unguwa dama,mama ta fake da cewa tunda uwar asugwui na zuwa wai inna take nufi su suyi zaman su base sunje ba,da wnn mama ta hana umma zuwa gurin su Hafsatu.

Amma ita idan fitar ta ta  kamata tana zuwa gidajen ƴaƴan umma batareda ta sani ba.

Kande a hanyarta ta dawowa daga kasuwa tana shirin tsallaka titi amma an tsayar da kowa daga masu ababen hawa har masu tafiya aƙafa,wasu irin maka makan motoci ne na sojoji baƙaƙe suketa wucewa aguje, tana tsaye agefe tana kallo,se masifa take wai an hana su wucewa saboda wasu banzaye masu baƙaƙen kaya,wai su sojoji,wanda tasan yanzu idan zasu ga bomb ba wanda ze tsaya guduwa za suyi "mtswwww*,taja wani dogon tsuki tana cewa "ai wlh idan jarumin soja na gaske akeson gani abari nazama soja za aga jarumta, duk wani bomb ko wata AK47,dasu igwa,dasu gurnet,dasu tiyagas da waye bazasu bani tsoro ba,kai woo ni woo ni,zaa kand zaa ƙanwar mazaje su ustazu Hamis dasu ya Musa,zaa 1 nd only soja of gidan ustazu habu me kayan koli yihuuuu cau cau" ta fada tana wani jijjiga ita bata yadda ba itama namiji ce kuma soja ce, kallonta na kusa ta ita sukayi suka kwashe da dariya.

Ihun mutane suke yi ganin wani mahaukaci ya karto aguje ta cikin jerin motocin nan yanaso ya tsallaka,cikin rashin Sa'a motar ta bigeshi,ai aguje kande ga saki kayan hannunta aƙasa ta ratso cikin mutane tana "kai ku kauce" har ta iso gaban mahaukacin nan wanda yake ta juya kansa daya ɗan fashe ga gwiwar hannunsa ma ta ƙuƙƙuje,saurin tsallaka wa tayi inda mahaukacin yake zaune se yamutsa fuska yake alamar yanaji zafin ciwon nasa,tsugunnawa tayi ta kama kan nasa ta ɗago tayi saurin yago gefen burmemiyar rigar jikinta ta ɗaure masa kan nasa,mutane anci dafifi ba wanda ya isa inda suke se kallo ake ana mayarda yacce akayi,gasu tsakiyar titi ga rana,ga motocin nan dole suka dakata saboda basu gama wucewa ba mahaukacin ya ratsa har aka buge shi.

Kallonsa tayi tace "kai kirezi ina zaka je ne bakada farin tuwo ne acikin kanka iye?wai ƙwaƙwalwa ce farin tuwo,kana kallo kowa an saka masa pause saboda lakwaye zasu wuce amma ka wani taho aguje, inama zakaje ne,ba a area na baroka ba meya kawo nan?kar de sake biyo ni kayi?aiko gashinan ka samu riba Dilla miƙe kirezius kawai" se masifa take masa tana turancesa kamar yana fahimtar me take faɗa,kama masa hannu tayi ta miƙar dashi tace "taho na kaika gefe ka huta".

Wani soja ne ya fito cikin baƙaƙen kaya fuskarsa sanyeda face mask ya rike wata bindiga abar tsoro yana zare jajayen idonsa yace "hey u bunch of lunatics,bazaku tashi agurin ba?bakwa gani kun tsare mana hanya ne?"

Juyowa kande tayi tana kallonsa kamar bazata ce komiba sekuma ta tsaya tamasa kallon sama da ƙasa tace "me i no wasa da ragwayen sojoji lyk U,kuma kaine benci ba ni ba ɗan renin hankali kawai, ɗan wulaqanci ku bige mutum ko sannu baku ce masa ba sannan kawani taho ciki agaba kamar tankar miyau dawasu idonka kamar gautar ɗaci kanaso ka karanta min nonsenseus,eh r u mara foka living things kawai, ni bana tsoron ka ehe ,i no tsoronka" daga hannu cikin ɓacin rai ze mareta mutane se kallo akw,wasu ma tafiya suke amma sun tsaya kallon yacce zata kaya tsakanin wannan yarinyar me shigar maza,dan bazasu ce itama mahaukaciyar bace duba da yadda take tsaf tsaf,kawai shigar ta ce ta maza.

Tana tsaye ƙiƙam ko gezau batayiba mahaukacin nan kuwa hana tsaye a bayanta se ɓoye fuskarsa yake alamar tsoro yakeji,ya rirriƙe mata riga ta baya,ganin za'a mareta da sauri ya kama hannunta yana ja alamar ta zo su gudu amma kande da taurin kai ta fizge rigarta tace "Dilla cen cikamin rigata,idan tsoro kakeji koma gefe kayi kallo,ko kuma ka hau legediz Benz dinka ka ja saɓa,wannan kurtin sojan besan ni bane,nima fa banaji Allah wlh, Nima soja ce daka ganni anan kawai wannan kayan ne bana sakawa",ta fada tana juyowa kan wannan sojan,dede sanda ya sauke hannunsa caraf aka cafe hannun,juyowa ya yi yaga wanene wannan me rabon

shan wahalar,saurin ƙamewa ya yi yana sarawa wanda ya riƙe hannun nasa,yace "sorry boss,wannan mahaukatan ne suka tsayar damu,sun shiga kan hanya" yafaɗa har lokacin yana ƙame"

Kallon kande da taja daga wanda ya fito yanzu ya yi,yana sanye cikin wasu irin kaki na sojojin ciki wato elite force,ya ɗaure gashinsa da band baƙi,fuskarsa rufe da mask iya idon sa ne abuɗe,kallonta yake yadda take wank hura hanci taja ƙafa ɗaya baya ɗaya agaba ta dunƙule hannu kamar zata kai naushi, irin tana jiran kora kwana,matsowa ya yi kusada ita cikin wata exotic voice yace "sorry ƴan mata,bakuji ciwo ba ko?"  "Normal kawai oga,beji ciwoba ai bani aka bigeba wannan kirezin ne" tafaɗa tana wani karkace baki gefe tana hura hanci tare da nuna mahaukacin wanda har lokacin idonsa aƙasa yana ɓoyewa abayan kande, se wani sunkwi da kai yake.

Ƙura masa ido general Asim ya yi wanda sunansa yake rubuce agaban rigar kakin jikinsa,har lokacin be cire mask ɗin ba,kallon mahaukacin yake sosai kafin ya juyo kan kande yace "cool down soja girl yi hkr naga beji ciwo sosai ba ma,amshi wannan ki siya masa maganin ko a chemist ne" yafaɗa yana mikawa wannan sojan na ɗazu hannu, kuɗi ya miƙo masa masu yawa ya amsa yana miƙawa kande,amsa tayi tana wani ci cijewa ta ƙirge 5k ta miƙa masa sauran tace "wannnan ma sun isa,zan siya masa harda abinci ma,1k kuma na siyi waken soya na dana zubar nasan yadda ake yunwar nan wasu sun kwashe" kallonta kawai yake be amsaba ta ajiye akan wata mota dake kusa dasu tace "censa yakkaɓai na sara maka,naga kamar kai nagari ne,mazan fama Allah tsare gaba da bayanka, banda wasu masu neman dukan talakawa,censa yakkaɓai" yafaɗa tana sara masa,amma wai yakkaɓai zatace masa.

Shide yana tsaye yana kallon ikon Allah tajanyo hannun mahaukaci wanda g.Asim keta ƙarewa kallo sukayi gaba, mutane se kallon kande ake ana mamakin ƙarfin halin ta,haka ta dinga tsara mutane tana wucewa janye da hannun mahaukaci wanda yake ta rawar jiki kamar yanajin tsoron mutane.

Komawa mota su g.Asim sukayi suka ƙara gaba.

Haka kande ta kai mahaukaci wani chemist aka wanke masa ciwo se yatsina fuska yake,kande na gefe tana yi masa sannu cen tace "Dilla jishi ƙato da kai se wani kwaɓe fuska kake,bawani zafin kirki nasani, kuma ma wai ina ƴan uwanka ne suka barka se galantoyi kake  layi2 kwararo2,koda yake ma kaida kake kirezi ina zaka sani" haka ta dinga ɓaɓatu me Chemist nata dariyar yadda take wani buɗe kafaɗa take ita adole najimi ce.

Ana gamawa ta biya kudin taje bakin masallaci ta siya masa shinkafa da wake me mai,ta siya masa kifi soyayya ta saka aciki ta sai nasa fanta ta haɗa ta kawo masa,ko wanke hannu be jiraba ya zurma hannu yafara kai loma hannu baka hannu ƙwarya.

Kallon sa take seya bata tausayi tace "oo kirezi anji gumama, kai wlh yunwa arniya ce baruwanta da hauka ko kai yaro ne,kawai kowa farmaka take,kai yunwa Allah gama mana dake arniya kawai" idan ba gizo idon ta ya yi ba kamar murmushi mahaukacin nan ya yi,amma se taga kamar idonta ne,yana gamawa ta zuba masa ruwa ta ɗau gorar da ya shanye fanta ta watsa maganin da me Chemist ya basu ta zuba ruwa ta jijjiga yana narkewa cikin dabara ta baiwa mahaukacin nan aiko ya amshe ya shanye ba musu ta kalle sa tace "kai kirezi a haka de kamar me hankali, duk yacce akayi da kai ba wata damuwa,kuma dan Allah duk ƴan uwanku aka rasa wanda ze kula dakai,nagade ba ka duka balle suce, yaude nayi aikin lada,dole ma na faɗawa su zakarius".

Seda ta ga ya fara bacci aƙasan bishiyar mangoro da suka zauna sannan ta tashi tace "barin ware nide,gashi bakada suna to korezi se anjima na saɓe".

Hartayi nisa mahaukacin nan be dena kallonta ba,idonsa cike da hawaye.

Bayan inna ta gama kulawa da hafsatyta mata duk wani abinda yakamata tamata sallama ta wuce asibitin mlm Aminu Kano gurin Maryam wacce take nan rai a hannun Allah, ta kasa haihuwar abin dake cikin kula ga haihuwar,duk ta galabaice ta fice a hayyacinta, tana ganin inna ta fashe da kuma tana rike hannun innar tace "kuyafemin inna mutuwa zanyi,dan Allah kice mama da baba su yafe min,momy da Abba kuma ku yafe min dan Allah mommy kicewa Aliyu shima ha yafemin" tana gama faɗa tafara salati,da sauri inna ta ciro ruwan addu'ar da mlm yabata ta kafawa Maryam abaki wani ya shiga wani ya zube haka har tasha kusan rabi,mintinan goma tsakani tafara wata irin jijjiga kamar convulsion ya kamata da sauri mommy sarakuwar Maryam ta fita ta kira nurses suna zuwa sukace kowa  yafita abasu guri.

Kafin awa daya Maryam ta haifi abinda ke cikin ta ashe twins ne gasunan kamar ƙadangaru haka aka nannaɗe acikin tsumma aka baiwa daddyn Aliyu dan shi Aliyu mijin Maryam baya gari yana hanyar dawowa.

Tasamu bacci,acen inna ta wuni har dare, koda kande ta koma gida bataga inna ba agurin mlm ta tare se addabar sa take da sheri kala2 tana masa zancen bazawararsa batula,anan unguwar take tana mugun son mlm habu,hakan yasa duk inda taga kande yi take kamar ta mayar da ita

cikin ciki.

Se dare kusan taran tare inna ta dawo,koda ta dawo ta samu kande tayi bacci a ɗakin Amo.

Zaune take agaban madubinta na tsafi ta saka doguwar rigarta baƙa wacce take sawa idan zasu gana da bokanya mama,cikin ɓacin rai da murya me firgitarwa mama tace "Zabba'u babu yadda za'ayi aikin ki ya yi kyau bayan kin zauna kina bacci,an toshe mana duk wasu hanyoyi da zamu kuma samun galaba akan ƴaƴanki,daga yanzu bazamu kuma samun damar sadaukar da jininsu wa dodo ba,sannan ƴarki siddiƙa ba abinda zamu iya yi mata,na gargaɗeki akan karki yadda kowa ya ganki alokacin da kike birne mahaifa da kuma jinjirin karyar nan,kin karya mana doka saboda haka dole ki karɓi hukuncinki"

Cikin matsanancin firgicin mama take cewa "kitemakeni yake mama Ajuji yaja da zamaninki yake mama me tukunyar Sheri,wallahi bansan yadda akayi hakan ta kasance ba,bansan wanda ya ganni ba a sanda nake aiwatar da aikin,seda na tabbatar kafa sun kau kafin na aiwatar da aikin,sannan bansan taya aka toshe mana hanyoyin baiwa dodo Ajuji jinin su Hafsatu ba,mama kitemaka min,abani wani aikin komin hatsarinsa inde ƴata siddika zata dawo cikin nutsuwarta to koma meye na amince zanyi".

Ɗago kai mama bokanya tayi baka iya hango fuskarta sam,se wani abu jaa sosai kamar garwashi wanda yake nan kamar idonta,cikin muryarta me rarrabuwa tace" babu wani aiki da zaki aiwatar da ze ceci ƴarki,tun farko mun gargaɗeki amma shashancinki da banzan tunanin ki yabaki cewa ke kaɗai ce me jiran duhun dare domin aiwatar da buƙatarki,saboda haka a yanzu de babu abinda zamu iya miki,karki kuma nemana idan ba abu me muhimmanci kika zo dashi ba"

Jiki a sanyaye mama ta rufe madubin ta na tsafi,kuma ta duƙufa acikin tunanin neman mafita,tabbas ko ya zatayi seta ga bayan A'isha,tunda suka taso a rayuwa itace matsalarta, tunani tafarayi rahuwarta ta baya.

FLASH BACK..

Zabba'u mama da A'isha Inna,maƙotan juna ne kafin suyi aure,tun suna yara ba wani jituwa suke ba Allah be haɗa jininsu ba sam,haka kawai Zabba'u ta tsani A'isha batareda wani

ƙwaƙƙwaran dalili ba,irin tsanar nan ta rashin haɗuwar jini marar tushe.

Islamiyyarsu ɗaya, Zabba'u ta girmi A'isha,amma A'isha na gaba da ita a makarantar islamiyya,saboda ƙoƙarin A'isha itace head girl a lokacin,wata rana tana tsaron latti abakin gate itada ƴan uwanta prefect Sega Zabba'u da tawagar ƙawayenta ƴan salon tsiya kai ba kokari,haka sukazo kansu tsaye zasu wuce amma prefect din nan sukace dole se an musu bulalar latti,nan fa faɗa ya ɓarke harda dambe A'isha na gefe duk masifarta bata fiya dambe ba,dan irin mutanen nan ne masu zuciya da nacin faɗa,kuma inda tasaka maka hannu seta fitar da jini,hakan yasa bata fiya dambe ba.

Tafiya tayi ta sanarda shugaban makarantar alokacin yana meeting da wasu malamai da alarammomi akan musabaƙar da za'ayi yana basu sunayen ɗalibai masu hazaƙa,acikin malamai baƙin fuskar da sukazo makaranta harda mlm habu,acikin ɗaliban kuwa harda A'isha,da sauri shugaban ya tashi ya biyo bayanta, haka ma mlm habu,koda sukaje sun samu Zabba'u tacire hijab ɗinta se tiƙar dambe take da prefects ɗin,yaranda tama girmesu,aikuwa nan da nan shugaban makaranta ya tattara su zuwa Ofishin sa, aka tmby meya faru nan fa kowa ya hayayyaƙo tana bada bayani,kowa nason ace shine me gsky, A'isha na gefe batace komi ba,buga musu tsawa shugaban makaranta ya yi kafin ya juyo kan A'isha yace "head girl Muna sauraron ki meya faru?" Nan ta kwashe yadda akayi ta fada cikin nutsuwarta kanta a sunkuye, nan shugaban makaranta ya baiwa wani malami bulala yace ya zane masa su Zabba'u,aiko agaban baƙin malaman nan aka zanesu se sharɓar kuka suke amma Zabba'u ko gezau batayiba duk da yadda bayanta ke raɗaɗi dan sun daku, kuma shugaban makaranta ya fi ga musu faɗa harda ce musu manyan kawai,da ƙannen bayansu suke faɗa,A'isha na gefe tana murmushi, Zabba'u kamar ta tashi ta shaqe A'isha har lahira,bada ita akayi faɗan ba amma duk t fi jin haushin A'isha akan kowa.

Bayan sati ɗaya aka fara zaban ɗaliban da zasuje musabaƙar state,A'isha ce farko acikin list ɗin,bayan an watse daga assembly Zabba'u tasamu shugaban makaranta tace masa itama tana son shiga,haka ya sanya sunanta aka haɗasu da wasu malamai wanda bana makarantar ba suna musu rehazal da testing ɗin karatunsu don jin wanda ya zama colified aje dashi musabaƙar,A'isha ta haye tare da wasu maza biyu,dama mutum biyar ake buƙata,amma Zabba'u ko zango na farko bata wuce ba,gashi ta nace seta yi abinda A'isha tayi sbd sanya wa rai wahala,duk wannan abin da takeyi ustaz habu farin malami me zazzaƙar murya tare da cikakkiyar ƙwarewa akan iya sarrafa karatun Alkur'ani shine yatafi da imanin Zabba'u.

Duk wannan naci da fafutukar shi take wa,amma kamar ma besan tanayi ba,dan ko kallon fuskarta bayayi.

Haka Zabba'u tazama discolified a cikin masu zuwa musabaƙar nan, antafi kuma makarantar su itace taciyo wa Kano ta ɗaya,har kyautar maka da kuɗaɗe masu yawa A'isha ta samo,haka aka dinga murna aka shirya walima akaci aka sha,A'isha ta baiwa abbanta kyautar kujerar hajjin da aka bata.

Kawayen Zabba'u babu wacce batasan irin mugun son da take wa ustaz habu ba,har kirari mata tare da canza mata suna,ZAHAB shine sunan da tamayar wa kanta,ba wanda ya fahimci abinda ake yi,daga ɗalibai har malamai balle shi kansa uban gayya mlm habu,kwatsam aka kawo cingum da alawa anata raba wa ɗalibai wai anyiwa ustaz habu baiko da A'isha head girl,....

Aranar har wata iskar bala'i Zabba'u ta hau,aguje ta damƙi wuyan A'isha wacce take zaune a aji se tsiya ake mata wai dama soyayyya suke da ustaz habu amma ba wanda yasani,ƙawayenta sun sata agaba da zolaya ita kuma se sunne kai take tana dariya,ba zato Zabba'u ta shaqi wuyanta,anyi anyi arabasu amma abu yaci tura,se ihu ɗalibai keyi, wasu kuwa aguje sukeje sukazo da shugaban makaranta,kamar haɗin baki sefa ustaz habu shika yazo makaranta kasancewar ba ana yake koyarwa ba,aikuma wani irin karfi ne yazo wa A'isha tayi wani irin kukan kura ta ɗaga Zabba'u sama duk da girman jikin ta amma A'isha sefa ta kaita ƙasa,haka tasamu sa'ar Zabba'u ta dinga naushin baki da hancinta seda ta zubar mata da jini bana wasa ba,koda shugaban makaranta da ustaz habu suka ƙaraso ai Zabba'u ta dena iskoki ta koma ihun neman agaji,ihu take iya ƙarfinta tana faɗin arabafa da A'isha mahaukaciya ce,dakyar da bala'i ustaz habu ya sanya hannu ya fizgo A'isha daga kan Zabba'u wacce tayi laushi,fuskarta ta haɗe da jini,bakinta hanci,idonta duk sun kumbura suntum.

Se fizge2 A'isha keyi tana sake kaiwa Zabba'u cafka amma mln habu ya riƙe hannunta sosai,har seda ta gaji dan kanta ta tsaya tana mayarda numfashi fuskarta tayi jajur,se huci take,haka aka ƙara tara wani taron a ofishin shugaban makaranta,anyi anyi da Zabba'u wacce keta rusa kuka ta faɗi abinda A'isha ta mata harta sameta da faɗa amma taƙi faɗa se kuka take rafsawa.

Wani mlm ne yaje ajinsu Zabba'u da nasu A'isha ya kira mutum uku2,ƴan ajinsu A'isha aka fara tmby meya haɗa Zabba'u da A'isha fada,sukace sude suna zaune kawai sukaga Zabba'u aguje ta damƙi wuyan A'isha ta shaqe ta,sunyi sunyi su raba amma sun kasa shiyasa sukazo suka kira shugaban makaranta.

Ƴan ajin su Zabba'u aka tmby ko sun san abinda ya faru,nan fa kowa ya fara zare ido,seda shugaban makaranta ya daka musu tsawa kafin suka fara inda inda, shugaban makaranta yace wa malamin ɗazu ya ɗakko bulala ya zane masa su,cikin tsoro sukace zasu faɗa.

Babbar ƙawar Zabba'u Hairatu itace tafara bayani,"um dama wai,am um mlm wallahi tsaya kaji,dama Zabba'u ce take son mlm habu,shine yau kawai se muka ji wai an musu baiko da A'isha".

Dumm haka gaban kowa ya buga harda Zabba'u wacce ta dunƙule agefe se gumi take,ga kuka tana kan yi.

🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
        *MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Not edited

Free page:10

Bismillahirrah manirrahim.

Tunda aka faɗi abinda ya haɗasu kunya ta kama Zabba'u,duk setaji ta muzanta,ace tana faɗa

akan namijin da bemasan tanayi ba, mlm habu kuwa tashi kawai ya yi ya bar makarantar ma gabaki ɗaya,A'isha kuwa wani irin tuƙuƙin baƙin cikin ne ya kamata wato akan masoyinta ma aka mata wannan renin wayon ko,shi kuma harda wani tashi ya fita kamar munafuki ai zezo gida anjima ya sameta.

Haka shugaban makaranta de ganin ba wani abin arziki bane ya janyo faɗan se son rai irin na Zabba'u da kuma Sherin zuciya,hakan yasa ya tilasta Zabba'u ta baiwa A'isha hakuri ko kuma tazo da iyayenta gobe,ai da sauri ta bata haƙuri,don gidansu ba wanda ze goyi bayanta idan sukaji abinda ya faru,wata kila ma asaka wani malamin ya kuma zaneta.

Sallamar kowa shugaban makaranta ya yi,ya rage daga shi se Zabba'u se malamin da aka tura kiran ɗakibai ɗazu,nasiha sosai shugaban makaranta yamata,tarefa ƙara lurar da ita muhimmancin kamewa agurin mace,duk da cewa dan taso wani ba lefi bane amma abinda tayi na jan faɗa lefine,idan kuma ta duba shi wanda take faɗan dan shi bemasan tanayi ba.

Godiya ta masa kamar abin kirki,duk taji ta muzanta,tun daga ranar bata kuma zuwa makaranta ba,har aikawa shugaban makaranta ya yi akace lafiyar ƙalau,kuma tace ace ita ta haƙura da makarantar gaba ɗaya.

Haka akasha bikin A'isha da ustazu habu, watansu biyar da aure,Musa ya yi aure shima,se bayan ankawo amarya ne A'isha taga ashe Zabba'u ce,itama Zabba'u data ga A'isha amma seta nuna kamar batasan inda A'isha ta fito ba,dafarko A'isha tayi binta da lalama tana girmamata matsayinta na matar wan mijinta amma daga baya ta tattara ta dena tunda taga abin na Zabba'u ba hankali aciki.

Baran ma da Mudassir ya yi aure,mama ta janye Hadiza matar Mudassir suka haɗe kai iskanci ba wanda A'isha bata gani,har kawo yanzu bata canza zani ba.

Sauke dogon numfashi tayi afili tace "A'isha kin aikata babban kuskure na shiga rayuwata da zame mini katanga da duk wani cikar burina, kuma zan nuna miki kin aikata babban kuskure, Ni dake shega ka fasa.

*_Bayan wata huɗu_*

Kande ce take tafiya tana ƴan waƙe waƙenta,tasha wata burmemiyar rigar me botira agaba,yau kam Amo harda guga tamata,ta fesa turare se tafiya take tana ɗage kafaɗa,hannunta riƙeda kuɗi da wani ƙaramin bakko zata kasuwar ƴan kaba, yau komai na kayan miya basu dashi,waken soyar ta ma ya ƙare shine aka ɗau na agwagwa za'a tafi kasuwa siyyya.

Gitfa wasu ƴan mata tayi,suka kalleta suka kwashe da dariya, ɗaya tace wa sauran "Allah na tuba,yanzu wannan wai mace ce amma duk ta lalata jikinta da tafiyar maza,ita adole namiji ce", ɗayar ma tace "waifa soja take kiran kanta"hhhhhh suka kuma sheqewa da dariya,ta ukun kuwa tace nide birgeni take wlh,ga kyau,wannan idan zata nutsu wallahi mace ce me zati da diri" ta farkon ta kuma cewa ke dilla cen matsa,ina wani kyau anan wacce kullum take wuni cuɗanya da maza,mtwsss" ta biyun ma ta kuma cewa "kyau iya kyau amma na banza ba mashinshini,ni wnn anya ma akwai nonon arziki aƙirjinta kuwa?" Ta fada tana kama haɓa, wata dariyar suka kuma sheqewa da ita suna tafawa.

Juyowa kande tayi afusace ta nufosu tana wani irin huci,tsayawa sukayi dan ganin me zata musu ita kaɗai sukuma har rai uku,tana zuwa ba wata2 ta haɗa kansu guri ɗaya dukansu,da wacce ke tsakiya da waɗanda ke gefe da gefe ta haɗe musu kai ji kake gub,agigice ta tsakiyar ta yanka ihu ta kwasa aguje kamar ta gigice, sauran biyun kuma suka tsugunna ko wacce tana dafe kanta dan sun gumu ba lefi, kallonsu tayi a sheqe ta nuna ɗayar tace "kikace ko akwai nonuwa akirji na ko?, to maza miƙe ko laluba kiji" tafaɗa tana finciko hannun budurwar wacce ta fasa ƙara tana bawa kande hakuri,fadi take "dan Allah dan Annabi kiyi hkr wlh Sherin sheɗan ne,dan Allah kiyi hkr,ni wlh bazan kuma shiga harkarki ba dan Allah kiyi hkr ",kande kuwa ta rike hannun budurwar chaf tace aifa seta taba kirjin taji ko akwai nono.

Seda budurwa nan tagalabaita saboda kuka,fuskarta duk tayi kace2 da kuka sannan ta saketa dan ɗayar tuni itama ta cikawa bujenta iska,tace "arniya ƙaramar ƴar iska kawai" ta juya ta tafi gun aikenta.

Tana tafiya tana tuna yadda ƴan matan nan suka rikice musamman wacce ta ruga aguje kamar ta gigice se murmushi take ita kaɗai,abin ya bata nishadi,shafar ƙirjinta tayi wanda take mance ma wai akwai wata halitta agurin, rintse ido tayi jin ta taɓa wasu halittu masu matuqar laushi,madedeta dan sunfi ƙarfin hannunta,amma yanayin yadda jikinta yake bata da faɗi ta sama se ta ƙugu ga yacce take tafiya a ƙobare hakan yasa bakowa ne ze iya gane yanayin cikar halittarta ba,uwa uba kuma shigarta,amma duk wannan abin bisa tilastawar inna yasa take

saka half vest acikin burma burman kayan nata,wnn ma yaƙara temakawa gurin ɓoye cikar ƙirjin nata,wanda idan ba ido kasanya mata ba ma sam bazakace tanada su ba.

Hura hanci tayi ta daki ƙirjin nata tace "munafukan abubuwa arnaye me zanyi daku ma,ni dama baku fito ba yasin,bakkuda wani use agun soja" ta wani cuno baki gaba,tana sake yin doro da bayanta irin karma akuma lura akwai su agurin.

Sam kande ita a yanzu halittar mata akanta bata birgeta,zata iya rantse wa tana mantawa ita mace ce se idan tazo kama ruwa ko yin wanka,dan tunda Allah ya sa ta girma ta cika mace bata taɓa yin jinin al'ada ba,shekarunta ashirin da ɗaya,zata iya rantse wa ma tamanta mata suna wani abu wai al'ada,dan idan inna tana al'ada ƙaryar mutum yagane,ko lokacin sallah ya yi seta waske,mlm habu ne kaɗai ze iya sanin tana cikin halin rashin tsarki,hakan ya ƙara sanya wa kande ta manta da wata aba wai al'ada,balle a yanzu da inna ta dena yi kwata2.

A dede wani lungu wanda ze sada kande da kasuwa taga wani me baro a kwance aƙasa yanata sheqa amai,jikinsa banda rawa ba abinda yake,da sauri kande ta matsa kusa dashi tace "subhanallahi sannu mlm, bakada lfy ne?" Be iya ce mata komi ba, ya jingine da bangon gurin yana mayar da numfashi,jikinsa se rawa yake idonsa ya yi ja sosai,daganinsa yanajin jiki,ga barronsa a gefe,da sauri ta tashi taje gaban bore hole ɗin dake kusada su ta ɗebo ruwa a wani bucket data gani agurin ta kawo masa tana masa sannu,ya amsa ya wanke fuskarsa ya zuba akan sa,duk ya bata tausayi,a ranta tace oo Allah neman halak da wuya,kalli wannan babban mutum dashi amma yana na barrow,ko lafiya bashida ita amma ya fito neman halalinsa,* kande mutum ce me tsananin tausayi,ita kanta batasan tana da tausayi ba,wani abin ma bata sanin tanayi.

Gdy mutumin ya mata ya miƙe bayan yaɗanji karfin jikin sa,yaja barrow dinsa harya fara tafiya Jiri ya ɗebesa yafaɗi agurin a sume,da gudu ta tashi ta ruga ta isa inda yake a kwance ta na irin kiran bawan Allah,wasu masu barrow ta hango a tsallaken titi ta tallafo kansa tana bubbuga kumatunsa tana kiran bawan Allah bude idonka amma baya cikin hayyacinsa, tashi tayi ta ruga tsallaken ta kira masu barrow nan tace ga wani ɗan uwansu cen ya faɗi ya suma kamar ma bashida lfy ne,da sauri kuwa suka biyota zuwa inda yake kwance aƙasa a sheme,suna zuwa suka gansa da sauri ɗaya ya tsare musu napep suka kamashi daƙyar suka sanya aciki,dake sunada yawa se mutum uku suka shiga napep ɗin biyu abaya suka rikeshi se ɗaya ya shiga kusada direba suka tafi asibiti,sauran kuma suka zauna suka ajiye wa wanda suka tafi asibiti barrow ɗinsu,kande tana tsaye tana kallonsu har suka ƙulewa ganinta,jiki a sanyaye ta tashi ta shiga kasuwa tayi siyayyarta ta juyo hanyar gida,har lokacin fuskar mutumin nan me barrow bata bar idonta ba,duk tausayinsa dama talakawa ya rufe ta,ita de tasan su bamasu kuɗi bane,amma sunada wadatar da abinda zasuci daa na bukatar yau da kullum be gagaresu ba,harma wani kan iya jingina dasu shima ya wadata.

Tana tafiya tana tunanin halin tsadar rayuwa da yadda talaka kullum yake shan wahala,kamar ance ta ɗaga kai kawai idonta ya faɗa cikin na mahaukacin ta data sanya wa suna kirezi.

Ta daɗe bata ganinsa,kusan sati biyu rabon da ta gansa,amma da kullum yana biye da ita duk inda zata to seta gansa agurin, ta danganta hakan da kila dan tana bashi abinci ne,se kuma a ka ɗauki sati biyu bata gansa ba se yau.

Suna hada ido aikuwa ya sinne kai kamar ya yi rashin gaskiya,tsallaka titi tayi tashareshi ta nufi hanyar gida,kamar yadda tayi tsammani kuwa yana bayanta yana binta a hankali,amma suna da nisa da juna,wata kwana tashiga,ta ɓoye ta ɓace masa,ai kuwa aguje ya rugo ya biyo kwanar shima yana dube dube alamar ita yake nema.

Be ganta ba kawai ya kwaɓe fuska ya ɓata rai ya juya ze wuce kawai ya ganta a bayansa tace masa "woooooo" ,kamar ba mahaukaci ba seda ya firgita dan babu zato ya ganta akusa dashi,dariya ta fara ƙyaƙyata wa ganin yadda kirezi ya firgita se zare fararen idonsa yake,a sace ya saki murmushi shima se kuma ya kwaɓe fuska ya sauke kai alamar fushi yake,dariya take seda tayi me isarta yatsare ta da manyan idanuwansa yanata kallonta,baƙaramin kyau tayi ba yadda take sheqa dariyar,1 side dimple dinta kamar a zuba abu aciki ya zauna tsabar yadda ya loɓa, kallonta yake sosai ya shagala,ji yake kamar ya shafa kyakkyawar fuskarta,gashi ta ta sharɓa basilin ga hasken rana yana haske fuskarta se wani walƙiya take kamar wacce take amfani da glowing products.

Gimtsewa tayi tace "hi kirezius Ina ka shige ne?,2 sleep I no see u,were u go, eh" na sha ma ƴan uwanku ne suka kwalfeka,ashe de har yanzu kana nan a layi kana gararamba".

Ko mi be ce mata ba se sunkuyarda kai da yayi,kama hanya tayi tace "kai kirezi yau banda ko asi kawai ka ware nima nayi nan",ta kama hanyar gida,kirezi kuwa yau duk inda kande ta saka ƙafa shima seya saka,tayi2 ya tafi yaƙi,duk inda ta wuce se an kauce ganinta da mahaukaci,ko ita kaɗai ba me tarar hanyarta balle yau an ganta da mahaukaci,har gida ya bita,a ƙofar gida Ikilima ta fito taci kwalliya da alama fita zatayi,se yauƙi take tana wani gyatsine,tayi kyau abinta itama fara ce kyakkawa,yanzu ta gare shiga shirgin kande tauda de taga ba riba,koda yaushe idan ta haɗo su itace take shan wuya,kuma ba wani mataki da ake ɗauka shiyasa tayiwa kanta karatun ta nutsu.

Ai tana hango kande da wani rusheshen mahaukaci ta tsallara ihu aguje ta koma cikin gida tana ihu,malam dake zaure da dalibansa da sauri suka fito waje dan ganin abinda ya tsorita Ikilima haka,ai kwa darewa suka farayi suma ganin kande da wani ƙaton mahaukaci.

Tsayawa tayi tana cewa "kirezi tsaya anan barin gani ko inna ta gama tuwo,kuma kana cinyewa

ka kama gabanka tom", kamar me hankali yako tsugunna agurin,mlm habu yana tsaye yana kallon ikon Allah.

Juyowa tayi zata shiga gida taga mlm da ɗalibansa sunyi cirko2 suna kallonta.

Sallamar ɗaliban mlm ya yi bisa dole,kafin ya janyo hannun kande yashiga da ita cikin gida,ɗaki ya kaita  ya nemi guri ya zauna ya ƙura mata ido,kallonta yake sosai itama kallonsa take cikin ido,kallonta mlm yake yana karanta wasu addu'o'i itama kallonsa take ido cikin ido,sosai mlm yake addu'o'in nan,idonta ne yafara tara jini nan take idonta yakoma kamar an zuba nuna mata jini,saurin rintse ido tayi gumi na karyo mata ta ko'ina.

Cikin buɗaɗɗiyar murya ta fara magana hankali kwance,tace....

# 🌹kANDE🌹
(_The tomboy_)
Paid book.

Na.*SADIKA IBRAHIM.*
*MOMSANI*

*Marubuciyar*:
# saurayin yayata free
# sirikara free
And now
# kANDE paid.

Not edited

Free page:11

Bismillahirrah manirrahim.

Cikin buɗaɗɗiyar murya ta fara magana hankali kwance,tace "malam Abubakar bin Hamza,meyasa ka kasance me gaggawa ne a wasu lokuta? Tabbas kai ɗin cikakken ɗan Adam ne, gaggawar ka ta kuma tabbatar mana da hakan,idan baka mantaba abaya shekaru sha ɗaya da suka shuɗe mun taɓa faɗa maka akwai sirri dunƙulalle a tattare da goɗiya,to a yanzu sirrikan sun  fara bayyana tabbas wannan mahaukacin ba mahaukaci bane, cikakken mutum ne me hankali,kuma ba ƙaramin mutum bane,sannan ta dalilinsa ƙofar sirri zata buɗe,mun baka gajeren  haske,sauran kuma kaine da kanka zaka nemo,tabbas kai ɗin ubane na gari,kuma kaso abinda bakada alaqa kota kusa bare nesa,tabbas zakaga sakamako,mahaukaci sunansa A'ZAM(ma'anar sunan the greatest),ka tunkaresa kai tsaye kuma ka nuna masa kasan yanada hankali,tabbas zakasan duk wani abu da kake da buƙatar sani,dukkan wani sirri ze bayyana,amma ko ka sani lokacin bayyanar sirrin wa goɗiyar beyi ba,kai kaɗai kake da damar sanin wannan sirrin,.. malam Abubakar bin Hamza tabbas zakaga sakamakon alherin ka,ka bar damuwa da yanayin rayuwar goɗiya,tunda kayi hkr na tsawon shekaru to haƙiƙa ribar ka akusa take,komi ya kusa zuwa ƙarshe,sannan sirrin cikin gidan nan ma ya kusa bayyana,duk ka zuba ido zakayi kallo kuma zakayi mamaki,abinda ka sani da wanda baka sani ba duka zasu fito fili,Ni  zan tafiiii,kuma zan dawo kamar de yadda aka saba".

Hamma me tsayi kande ta yi kafin ta lumshe idonta a hankali kuma ta kwanto a jikin mlm, maida hannunsa ya yi ya rungumeta idonsa na zubar da hawaye masu zafi,tabbas shi yasani dole wata rana abinda yake gudu ze faru,amma be ɗauka abin a kusa yake ba,ji yake kamar bayason wannan ɓoyayyen sirrin ya bayyana,inama wannan abin da suka binne ze iya zama sirrin da har abada baze bayyana ba,inama inama,amma ba yadda ya iya,shi yasani dole ne abinda yake gudu seya faru,yasani wata rana dole hakan zata kasance.

Kallon kyakkyawar fuskar ƴar tasa ya yi wacce ta jiƙe sharkaf da gumi,jikinta duk ya saki,juyowa ya yi ya kalli inna wacce ta takure se sharbar kuka take,tunda aljanin kande ya fara magana ta shigo ɗakin,dan ta zaga ne sanda mlm ya shigo hannunsa riƙe da kande, fitowar ta ne ta gansu acikin yanayin da kande bata hayyacinta.

Itama taji duk abinda kande ta faɗa ko  ace iskanta ya faɗa.

Shimfiɗera mlm ya yi,seda ta kai kusan magrib tana bacci kafin ta tashi a gajiye, jikinta duk ya mutu,akasalance ta kalli inna da Amo wanda suke zaune akan ta hannun Amo da carbi,se ja take tana zare ido,duk a tsorace take,kamar ace kyat ta fece aguje.

Inna kuma hannunta riƙe da wayarta keypad ta kunna kira'a sun ajiye a gefe.

Da sauri kande ta tashi zaune,tace subhanallahi inna karfe nawa ne,kallon juna inna da Amo sukayi kafin inna tace "karfe Shida da hamsin ne auta, ya akayi ne?,me za'a kawo miki kici?", saurin miƙewa tayi tana faɗin "innalillahi,inna garin yaya nayi bacci me yawa haka kuma baki tashe ni ba,wlh wani mahaukaci ne yaketa bina, kullum duk inda naje seya bini,ko dan ina bashi abin ci ne,yau ma har gida ya biyoni,nace zan duba ko kin gama abinci in bashi,ashe kwanciya nai, kai innalillahi,Allah sarki kirezi kilama ya tafi" tayi maganar a shagwaɓe kuma sak muryarta tun tana yarinyar ta kafin ta haɗu da lalurar iska.

Kallon Amo inna tayi,itama haka,duk da cewa Amo bataji me kande ta ce ba sbd kunnenta,amma yadda kanden ta kwaɓe fuska cike da shagwaba yabata mamaki,balle inna da ta ji abinda tace da kuma yanayin yadda muryarta ta fita,cikin ɗan murna wacce ta fara kama inna tare da tunanin ko addu'ar su ce ta karɓu ta ce "mahaukaci kuma auta a ina kika samo sa ke kuwa?" Kamar an mintsineta tace "Allah wlh kuwa inna,wani kirezius ne ya mini ta kaska,duk inda na dire legediz dita seya ɗora tasa agun,bansan shi bafa, amma ya nanemin,duk inda naje yana biye,shine yau ya biyo ni harnan da alama tsumagiya ce ta fyaɗosa,dan be taba biyoni har gidaba se yau," ta dubi inna wacce jikinta ya yi sanyi murnar ta ta koma ciki ganin yadda ta kuma komawa kanden ta me kamar maza,ta kuma cewa "ya ake ciki ne tuffar dagus akwai tuwon ne na ɗan sanmasa ya lomata shima?,kila ma ya tafi yaganni shiru kamar an aiki bawa garinsu, Allah sarki kirezius" ta fada tana sakkowa daga kan gadon.

Acen waje kuwa bayan mlm ya fita,da sauri ya leqa waje dan tabbatar da abinda aljanin kande yace,wayam ba kirezi ba alamarsa, jinjina kai Malam ya yi,tabbas wannan mahaukacin akwai ayar tmby akansa,amma tunda yake bibiyar yarinyar sa yasan dole da manufa,kuma dole ze dawo,yanzu dole shima yasaka ido sosai akan ƴarsa.

* Niger state minna*
_mariga way_

Tafiya suke amotar sunata mayarda zance akan yadda sace sacen mutane yazama ruwan dare,kawai se a ɗauke mutane ayi daji dasu kamar dabbobi,wasun su suna ganin lefin gwaunati ɗari bisa ɗari kan taɓarɓarewar tsaro,ga tsadar rayuwa kullum rayuwa daɗa ƙunci take,kullum talaka shine a wahala amma dan ɓacewar basira da rashin lissafi da talakan de za'ayi amfani asakasu su yaƙi junansu,su kashe junansu,hallau acikinsu ne ake samun waɗanda sunfi ma masu garkuwa da mutanen bala'i wato informants.

Wasu suka suna ganin kawai mafiya aksarin kidnappers son zuciya da dogon buri ne yake sanya su faɗawa cikin harkar,sunyi nisa sunata tattaunawa akan matsalolin rayuwa,ba zato sukaji direbansu yaja wani wawan birki yana salatin duk da yazo bakinsa, faɗi yake "yau munshiga uku tamu ta ƙare kowa yayi ta kansa,se a sannan kowa ya lura da abinda ke faruwa agurin.

Motoci ne iya ganine hange,duk an fitar da mutane an tarasu aguri ɗaya kamar shanaye,wasu mutane ne sun rufe fuskar su da baƙin abu,jikinsu sanyeda kayan sojoji,mashinansu kusan guda hamsin fake agefe daya,wasu mahaukatan bindigogi ne ahannun su,se fitar da mutane suke daga cikin motocinsu suna tattara su gefe ɗaya,cikin sanɗa direban wannan motar ta saulale ya fice daga motar yabar fasinjoji sunata sallallami,direban nan yana sanɗa acikin ciyayi yanason ya samu ya gudu,ba zato yaji bindiga akansa an ɗana masa ana cemasa ya miƙe ko a harbesa.

Cikin tsananin firgita ya miƙe tsaye yana haɗa me bindigar da Allah karya kashe shi,wlh yanada iyalai da marayu wanda suka dogara da shi,kaɗashi akayi tare da sauran fasinjojin da ya kwaso har inda aka tara mutanen da aka fara kamawa,yana juyowa idonsa akan wanda ya sanya masa bindiga,cikin tsananin mamaki yaga ɗaya daga cikin Mutane da ya ɗakko ne, wanda dashi akayi ta zancen ƴan garkuwa da mutane,ashe shima ɗaya daga cikin su ne.

Kusan duk motocin da aka kama acikin fasinjojin akwai kidnapper aciki,sune suka Sanar da ƴan uwansu nakan hanya cewar motoci sun taso da yawa,kasancewar ranar cin kasuwar mariga ne,har sukayi nasarar kame mutane da yawan gaske,mafiya yawancinsu ƴan kasuwa ne,wasu da kayan da zasu kai don cin kasuwar,wasu kuma da uwar kuɗaɗe ajikinsu don zuwa cin kasuwa,amma cikin hukuncin Ubangiji duk anyi garkuwa da su.

Seda ƴan bindigan nan suka haɗa mutane masu yawan gaske,kafin suka kaɗasu zuwa daji,bayan sun amshe musu kuɗaɗe da kayan abinci,haka suka tasa ƙeyar jama'a da dama.

Ga tafiya ba karama ba,wasu a hanya sukayi ta suma,wasu harbinsu akayi saboda sunyi yunkurin guduwa.

Seda sukayi tafiya me nisan gaske wacce ta shafe awoyi da yawan gaske kafin su isa wani ƙaramin gari inda ƴan bindigan sukeda zama,haka aka dinga amsar numbobin iyalan bayin Allahn nan ana kiran su ana sanar musu anyi garkuwa da ƴan uwansu,duk wanda akayi cinikin sa haka za'a waresa gefe,haka suka dinga cinikin mutane kamar dabbobi.

Wadanda ba a samu cikakken bayani agurin ƴan uwansu ba,da waɗanda sukace su basu da kowa suma aka waresu gefe,su nasu hukuncin na daban ne,mafiya yawansu saida sassan jikin su ake,wasu kuma kashesu ake,wasu kuma se ajuyar da tunaninsu suma su koma ƴan bindiga.

*******

_United Arab Emirates _
DUBAI.

_Durah jungle _

Dubai special force vanguard.

Wasu manya manyan sojoji ne da hukumar soja ta dubai suka ware waɗanda ake baiwa horo na musamman,a wuri na musamman,durah jungle wani sansanin soja ne dake nesa da garin sosai,su waɗannan sojojin bakowane lokaci ake fita dasu aiki ba,duk wani aiki me mugun haɗari shine aikinsu,kamar shiga ƙungiyoyin manya manyan daba irinsu, ISIS, mafias,ko kuma manyan sindicates wanda suka gagari duniya,irin wannan aikin ake tura su domin kawo ƙarshensa,chief commanda RAYYAN RAHMAN,shine tsaye yana kallon yadda atisayen ke wakana, tabbas lokacin da yake jira ya kusa ƙaratowa,shi da wasu zaƙaƙwuran sojoji irinsa wanda suka wahala kuma suka bautawa ƙasar su,sune suka fitar da wannan reshen na sojojin sirri tare da goyon bayan shuwagabannin kasar na ƙwarai.

Ofishin sa ya koma ya fara fitar da list na sunayen waɗanda za'a tura domin zama ɗaya daga cikin ƙungiyoyin dabar da sune a jadawalin su a yanzu,su waɗannan ƙungiyoyin sun gagari duniya ta fannoni daban daban,a kuma ƙasashe mabanbanta,acikin ƙasashen da za'a tura waɗan nan sojojin akwai Dubai ɗin kanta se phillipines,China,south Africa, Russia,Ghana da kuma linjeriya kasarmu ta gado🤣.

_Nigeria,Kano state_

*Sannu kaji mamuda, jiki ya yi kyau ai alhamdulillah,kaida muka kawoka ranga ranga kamar zaka sheqa, baka fa san waye akanka ba,Allah sarki wata yarinya ce me shigar maza shigar ta ta gwanin ban dariya,ita ce tazo tace mana ga wani me baro cen ya faɗi,shine fa muka rankayo aguje ashe kaine,ai yarinyar nan ta temaka wlh,da wata ce guduwa zatayi taga mutum a

kwance kamar bashi da rai,uhum kaide mamuda Allah ya kara afuwa,wai nace mamuda bakada ƴan uwa ne,ni har yau kwananka biyu amma banga kowa yazo  da sunan dubiya ba da ga fanni ka?"

"Wlh jabir kacika ɗan banzan surutu,haba mutum yana kwance bashida Ify amma ka sanya shi agaba se famar ratattako batu kake babu birki,sekace an buɗe dam din ruwa,haba dan Allaha"

"Kaiko lurwanu daɗi na da kai kenan ka cika saka ido da yanƙwana mutum,haba kalli fa yadda ƴan matan cen suka kakkallo ni, se wani faɗa kake min acikin jama'a dan na tambayi mamuda ƴan uwansa,naga ai gsky na faɗa,tunda muka kwaso shi ranga ranga muka kawosa nan bawani daga nasa da sukazo da sunan duba jikinsa,kuma dan na tambaya shike nan nayi lefi haba du Allah du Annabi lurwanu".

Se cecekuce samarin suke a tsakaninsu,wanda aka kira da mamuda kuwa yana kishingiɗe akan gadon marasa lafiya ya lumshe idonsa,ƙala be ce musu ba amma duk abinda suke fada yana saurare,har suka gama faɗan nasu kuma suka koma fira.

..... Moscow, Russia....

Wani irin gidane cable front acen cikin wani guri wanda ya yi nesa da cikin garin Moscow ɗin,kusada wani madedecin tafki,wasu manyan security ne suke shawagi agurin,duka ƙofofin gidan masu password da thumbprint ne,wasu manyan motocine kusan guda goma sha ɗaya suka parker a waje gidan,biyar agaba biyar abaya,se wata golden lemo a tsakiya,kusan atare ƙofofin motocin suka buɗe banda ta tsakiyan wacce ta kasance lemo.

Kusan mintuna asirin kafin aka buɗe daya daga cikin ƙofofin lemo din,wani ingarman namijine ya fito daga cikin motar,jikinsa sanyeda wasu simple Pakistan wear farare tas,se wani madedecin makawuya daya naɗa akan hular kansa wacce take baƙa, ƙafarsa sanye cikin takalma sau ciki baƙake,hannunsa sanyeda wani danƙareren agogo me matuƙar tsada,fararen yatsunsa sanyeda wani zobe baƙi me fuskar zaki,ya riƙe wata sanda kamar da gold me shegen kyau se walwali take,saurin buɗe masa lema akayi saboda snow ɗin da ke sauka agurin.

Fuskar mutumin kadai idan ka kalla seka kuma kallo,mutum ne majiyi ƙarfi, ingarman namiji ne sosai,fatarsa har wani yello take,fuskarsa cike da beard me ɗaukar idon me kallo,yanada kyau me suna kyau*wild king Rolex*kenan,tafiya ya fara cikeda izza irinta maza majiya ƙarfi,duk inda ya gifta se securityn wurin sun rungume hannunsu ɗaya a ƙirji tare da sunkuyarda kansu.

Yana zuwa gaban main entrance na shiga gida kofar tayi scanning na idonsa,bakinsa ɗauke da fito ya danna kansa cikin falon wanda ya ɗauki ɗumi me daɗi da ƙamshi,wata matace zaune fara me dogon gashi ta juya baya,hannunta ɗauke da wata ƙatuwar mage fara me kyau.

Takawa yake yana nufar inda take zaune,bakinsa yana fito,yana isa inda take gaban wasu duwatsu masu ci da wuta irin room heater ɗin nan na jikin bango amma wannan wasu irin duwatsu ne masu kyau da sheqi kamar normal dutse suna fitar da zafi de ɗumama daki.

Hannu yasa yana shafar dogon gashinta me kala biyu baƙi da roɗi roɗi kamar fari kamar milk,ko gezau bata motsa ba,ya cigaba da shafar sumarta har zuwa dogon wuyanta,hannu yasa ya juyo da kanta da ƙarfi ya juyo da fuskarta...ba zato wayar ɗauko rahoto ta faɗi saboda ganin fuskar matar nan..

Jama'a kande ce faaaaa, a Moscow😱😱😱

End of free pages kuma book 1.
*************************
Shin menene  ainahin asalin kande?

Wanene wannan mighty wild king Rolex din?

Wanene chief commander RAYYAN RAHMAN?

Wani lokaci yake jira?

Wanene mamuda me barrow wanda ke kwance a asibiti?

Wanene general Asim?

Wanene mahaukaci kirezi?

Wai ma suwanene mlm habu da inna?

Wani sirri suka sani akan kande,wanda aljanin kanta yake yawan nanatawa?

Meye alaqaar da aljani yace akwai tsakanin kande da kirezi?

Wani mission ne RAYYAN RAHMAN ze tura special force ɗinsa?

*Duka wannan amsoshin suna dunƙule acikin littafin kande kashi na biyu wato book 2.*

# love
# hate
# crime
# black money
# soccery
# betrayal
# illegal trafficking
# smuggling
# comedy
# romance
# momsani✍️

_Ina masoyan MOMSANI ina wanda suka daɗe suna jiran wnn zazzafar tafiyar ta labarin kANDE,zaa kanwar maza,zaa soja,zaa kAND,to albishirinku yaude Allah ya nufa kuma yakawomu acikin wnn daddaɗan labarin me suna kANDE,bakijiba ne nace kANDE zaa tomboy_

_shin dake akayi daddaɗar tafiyar nan ta labarin Asma'u da Muhammad Mahii ,SAURAYIN YAYATA,kin karanta labarin SIRIKATA,ko a'a,to albishirinku yauma momsani tasake dawo muku da wani daddaɗan labarin me dogon zango wato kANDE THE TOMBOY,in Sha Allah hajiyata bazakiyi nadamar karanta wnn labarinba_

_zazzafar tafiyace me ɗauke da zazzafan darasi,tare da nishadi,haɗi da ban tausayi,tattareda zazzafar soyayya,gamida cin amana dakuma butulci,bazan cika baki ba,bakuma zan cikaku da surutu ba,amma in Sha Allah karki bari ayi wannan mysterious journey din batare dakeba_

*kANDE littafin kuɗi ne akan farashi me sauki, Naira ₦400 kacal,idan kin shirya ki tura kudinki fa wnn asusun0591819457 SADIKA IBRAHIM gt bank,seku tura shedar biya ta wnn layin 07088282153,se na jiku masoya,i promise u will never regret*

Masoya ƴan amana Sena jiku,mom sani tana jiran ganin kauna daga gareku,love you all😘